# Masarautar Sasanci cikin Al'umma


Ma'amulla ko tuntuba:
info@cfaithministries.org
kent.hodge@ cfaithministries.org
www. Cfaithministries.org


Hadi da godiya ga kungiyar dake Jos. Kun bautawa Allah da zuciyarku da kuma rayuwarku, kuma kun kaunaci mutanensa dare da rana. Hakanan kun bada rayuwarku cikin kauna.
Wadanda sukayi addu'a kuma suka taimaki wannan kungiya ta "Christian Faith Ministries": Mun gode domin kasancewar ku wani sashin wannan kungiya.
Da godiya domin karfafawar kowa da kowa.
Kent & Ruth
Febirairu, 2015


Diploma, Degree, Masters in Theology
Prof. Kent Hodge
Christian Faith Ministries
Domin wani bincike:
0803 838 3960
0803 249 0935

**Abinda ke ciki**

Wannan littafin ba yana kan "tauhidi" bane amma yana gameda yin rayuwa yadda Allah yayi a wannan duniya lokacin da yasa jikin mutane a matsayin Yesu Kiristi, kuma ya rayu a tsakanin mu. Wannan kuma ya hadu da irin dadewar rayuwar da mukayi a kasar Nigeriya, kasar da ta kowacce hanya tana nuna irin kalubalen da muke fuskanta a dukan duniya.

A farkon shekara 2010, muna kewaye da konannun gine-gine, da kuma dubbai da aka kashe a sashin mu cikin 'yan kwanaki da satittika, da kuma jita-jitan tashin hankali a kowanne sashi, daliban da suke a makarantar Christian Faith Institute, Bukuru, Jos, sukayi tambaya, "Yaya ikkilisiya ta farko suka fi karfin Tsanani?" Sai muka fara dubawa, kuma wannan binciken ya fara wata tafiya da ta chanza tauhidin mu, tunaninmu da kuma irin rayuwarmu sama da kasa.

Menene ikkilisiya ta farko sukayi? Sun kaunaci makiyansu, kuma suka kaunaci rayuwarsu har zuwaga mutuwa! Sunyi wannan ba domin suna da suna Masubi kawai ba: Su masubin Yesu ne, wadanda zasuyi kamar yadda yace kuma suyi kamar yadda yayi a hanyar binsa. Domin haka muma bamu fara binciken abinda Yesu yace kadai ba, amma domin muyi addu'a don aikata abinda Yesu yace.

Mutane da yawa sun sa kansu cikin yaki marasa kyau a biranen mu: Al'ummar Masubi da Musulmi suka rarrabu, ba tare da wata sadarwa tsakaninsu ba. Damuwar ta habaka kwarai. Dole a sake gina zumunta tsakani. Mun ga irin wannan hallakarwar, daga nan a tsakanin dukan kuma, ga matasa da yawa da yara babu wani abun hannun da zasu yi kuma babu wani bege domin rayuwar nan gaba.

Akwai labarai da yawa da suka shigo na yadda Masubi da Musulmi suka tsaya da karfi domin ceton "sauran 'yan'uwa". Dagan an wadansu daliban mu suka gano wani yaro dan shekara 6 daga iyalin Musulmi, an yarda shi kusa da makaranta. Suka cida shi, suka lura dashi kuma suka kaishi zuwa wani masallaci domin a maida shi zuwaga mutanensa dake wani kauye kusa. Wannan ma ya taba zuciyarsu.

Bayan nan, wata kungiyar mu ta ziyarci wani aboki musulmi, mutumin salama da kuma dattijo a wani kauyen musulmi a lokacin sallah, a matsayin alamar nuna abokantaka. Mutane da yawa sun kalli wannan a matsayin kasada a wannan lokacin, shiga da kyau cikin "Samariya". Daga nan kuma wani mamban kungiyarmu ya gayyaci wani dattijo musulmi zuwa ofishin maigida na, inda muka tattauna yadda zamu taimaki al'ummarsu koyarda karatun komputa ga matasan su, kyauta ba da kudi ba. Sunyi mamaki kwarai sukayi tambaya cewa, "Me yasa mukayi haka?" Amsar mai sauki ce: Yesu ya lura da mu lokacin da muke makiyansa, kuma ya gaya mana mu kaunaci makwabtanmu kamar haka.

A watan Mayu, 2014 wani kaunataccen abokin mu da ma'aikaci na fiye da shekara 20, aka kashe shi yayinda suke tafiya shi da maigidana a cikin motar da suke tafiya tare bayan da wadansu Fulani dake sanye da kayan soja a cikin daji suka aiwatar da wannan. Ta yadda miji na da sauran abokan tafiyar suka tsira wannan ikon Allah ne kawai. Lallai abun ya dame mu kwarai. Abunda mutane suke fuskanta kenan kowacce rana: wannan rashin abokinmu, dan'uwa, maigida, da kuma uba, da kuma rashin tsaron dukiya da rayuwarsu. Me za'ayi domin chanza rayuwar wadannan mutane da suke tunanin basu da wata hanya sai dai suma su nemi hanyar ramako?

Bayan bisnewar da kuma cikin tashin hankalinmu, dattawan musulmi da sukayi bakin ciki damu, suka dauki miji na da wani mambar kungiyar mu zuwa wani sashi na Bukuru da aka lalatar lokacin tashin hankalin 2009/2010, wani wuri da masubi basa zuwa. Da muna tunanin tsananin kan masubi ne kawai amma da muka ga banner da Masubi sukayi, da gidajen musulmi da yawa da aka lalatar, an maida mata da yawa sun zama gwauraye da kuma yara babu gidaje da iyalai, mun sami cewa Allah yana kiranmu a matsayin masubi mu chanza yadda muke rayuwa. Akwai babban gungume cikin idanunmu.

Makarantar koyarwa ta komputa ta matasan musulmi ta fara aiki a sashin Bukuru, hadi da ta biyu a Bisichi. Zumunci na karuwa hadi da salama ta kauna, aminci, musulmai masu aikin hannu da yawa wadanda suke cikakkun abokai da kuma jama'ar kusa na al'umma. Tare muka fara wata kungiya ta taimakon mutanen da suke cikin yanayin tashin hankali. Wannan kungiyar ta iya taimakon wadanda aka

yiwa laifi, duka musulmi da Kirista, kamar na tashin bomb na kasuwar Jos a watan Disamba domin biyan kudin magani da kudin Asibitin su. Mun bada taimako ga gwauraye da masu kokarin aikin gidajensu domin su cigaba da kokarinsu bayan rashin da sukayi. Iyali  cikin bukata, wadanda basu iya biyan kudin makaranta ba ko kuma biya kudin aiki na asibiti su sami taimako. Taimakon yana biyan bukatar ‘yan gudun hijira da kuma lura da miskinan yara: marasa gidaje, wadanda basa iya cida kansu, biyan kudin makaranta, kayan sawa, da kuma kaunar su, duk tanadawa al’ummar wurin.

Yawancin malaman mu da dalibai wadanda ke yin koyarwa kan aikin pasto sunzo ne daga wuraren sassan kasashen Boko Haram kuma sun sha wuyar rashin iyalai, abokansu, dukiyarsu da kuma rayuwarsu, lokacin da suke kokarin kawo iyalan da suka tsira zuwa wurin tsira. Lokacin da muke kokarin hakurin shan wahala tare da kuma taimakon abokanmu, mun sani cewa wahala da kisa duka sun faru ga Kirista da Musulmi, kuma yawancin lokatai Kiristoci sun sa hannu wajen ramako. ‘Yan’ta’adda sun kashe Musulmi da yawa, kamar yadda suka kashe Kiristoci, idan ma bai fi ba.

Wannan littafi kira ne ga Kirista mu taimaki ‘yan’uwa, taimakon wadanda yawanci basu da inda zasu je domin taimako.

Yawancin Masubi suna addu’a ne kan Musulmi, domin hallakarsu, kuma suna hana Masubin da suke son su nuna kaunarsu gare su. Yawancin Masubi sun bada gaskiya sosai ga makarkashiyar – Musulmi ne fiye da koyarwar Yesu. Muna ganin wannan maida martanin a kasashen duniya da dama, ba wannan sashin kawai ba.

A yau, daliban mu da suka gama karatu da yawa suna gina ikkilisiyu, yin wa’azin bishara, da kuma taimakon yawancin mutanen da suka sami kansu cikin wannan mugun tashin hankalin. ‘Yan ta’adda sunyi karfi da yawa da kuma makamai sosai, har ya kai ga yaki da sojojin kasa, kama kusan sashi guda, samun miliyoyin ‘yan gudun hijira da masu yawa da kuma yara marayu cikin bukata mai Tsanani. Kaunar Yesu ta wadannan dalibai da suka gama karatu ta fito da yawa kuma suka bi shi da farinciki, suna kasancewa a birane da kauyuka dake karkashin farmakin ‘yan Boko haram domin su bauta. Yawancin ‘yan ta’adda da yawa an matsa musu shiga cikin

kungiyar Boko Haram ne, domin haka ba zamu ki su ba. Wadansu sun sami ceton Ubangiji kuma sun sami shiga cikin makarantun mu na littafi mai tsarki.

Wadansu daliban kuma suna ganin ikon Ubangiji yayinda mutane ke karbar Kiristi cikin salama a wuraren da al'ummai ke yin yaki. Dattawan Musulmi da Kiristoci sun taru wuri daya domin su koya gameda mulkin Yesu da kuma hanyar rayuwa kuma suna rokar gafara daga junansu. Wani dalibi ya fadi gameda al'ummar da yake wadanda suka tsananta masa domin ya tuba, "na gafarta musu, amma ban da wani abunda zanyi dasu."Wannan ya fadi kome duka: yin gafara ba tare da wata zumunta ba, wannan lallai ba ainihin gafara bace.

Wata daliba daga sashin Fulani ta zama makahuwa bayan wani hari, kuma ta kasance wata 6 a wannan matsayin. Dukan kokarin asibiti bai taimake ta da wani abu ba. Dalibai suka cigaba da taimakonta, kuma wadansu suka gaji. Sai mijina ya fada musu cewa, "Yayinda Allah ya warkar da mu, cikin hakurinmu na yin bauta, zai iya warkar da wannan matar."

Karshen wannan watan Disamba ta karbi wani nassi daga Ubangiji, a cikin littafin Mahukunta. Ta roki ma'aikata biyu su karanta mata wannan nassi kuma suyi mata addu'a. Wannan daren a dakunan kwanan mu da karfe 2:45 na safe, sai ta ga wahayin wani mutum yana fada mata ta tashi tayi tafiya, kamar abinda ya faru cikin bisharu. Sai tayi guna-gunin, "bana gani, don haka ina zan tafi?"Nan take ta sami warkarwa gaba daya. Wannan wani al'ajibi ne na wannan al'umma. Bayan labari ya fita, mutane Masubi da Musulmi suka taru domin su nuna godiyarsu tare.

Warkarwa ta cigaba da kasancewa a kauyukanmu kuma yanzu muna jin dadin salamar da ke cikin biranen mu. Ba kawai masu kisan kai na dasa bomb na 'yan Boko Haram ba (akwai su da yawa a nan a 'yan shekarun nan da suka wuce), basu sami ikon motsa wannan al'ummar zuwa mugunta ba, yayinda zukatanmu suka chanza. Yawancin mutane basu taba jin an hada Yesu da siyasa ko al'adu ba. Muna addu'a domin sakewa da chanzawar kasarmu yayinda yawancin Musulmi da Kiristoci suka sami motsawar ruhu mai tsarki kuma ya kawo su ga sanin ainihin Yesu kuma suka bishi tare.

Idan da shekaru 15 na tashin hankali na kasashen duniya da na wurare daban daban ya kawo wani abu, shine, cigaban tashin hankali ba shine amsa ba. Amsar kawai itace rayuwa kamar yadda Yesu yayi kuma ya koyar, gina al'umma, yin sulhu da juna da kuma gina mulkinsa na salama a cikin duniya da yin abu mai kyau ga mutane. Abunda wannan littafin ya kunsa kenan. Allah ya albarkace ka yayinda kake karanta wannan littafi.

Ruth Hodge, Janairu 30, 2015.

**Al’umma**

Zai zama tunani mai kyau mu fara da fadin dan kadan gameda abinda muke nufi da Kalmar nan al’umma. Ga wadansu, al’umma zai iya kawo musu tunanin mutane suna zama tare a irin yanayi ba lallai na aiki ba. Ga wadansu kuma, wannan zai iya nufin irin rayuwar ikkilisiya inda shugabanni suke gayawa mutane irin abinda zasuyi a al’ummar su. Wannan irin ra’ayi zai iya haduwa da kalma kamarsu “almajiranci”, wanda ga wadansu zai yi ma’anar kamar rayuwar dokoki wadda ke saurin juya aiyyukan rayuwa da tunanin kowa. Wannan ba shine muke nufi da al’umma cikin wannan littafi ba kuma ya kamata mu kiyaye tunani mara kyau bisa kan Kalmar al’umma.

A maimako, abinda muke nufi da al’umma yafi tafiya daidai da irin dalilin da muke da shi. Muna amfani da Kalmar da banbanci da akasinta, kamar, mutuntaka. Muna amfani da al’umma domin kwatanta dukan manufar ceton Allah: domin ya samu cikin iyalinsa mai kauna. Wannan wani abu ne da yake faraway da samun ceto. Shirin Allah na chanjin rayukanmu na cigaba yayinda muka bada shaida ga junanmu. Yayinda muke rayuwa cikin al’umma, wato, yayinda muka koyi kauna da lura da sauran mutane, domin bada dama ga sauran mutane da bukatunsu cikin rayuwarmu, daganan alamar Kiristi zata kasance a cikin mu. Shirin Allah shine kauna kuma wannan zai iya kawo chanji cikinmu gabadaya.

Wannan ya kai mu ga koyarwar Yesu cikin bisharar nan guda hudu. A cikin tarihin wannan zamanin, ya nuna alamar, yawancin babban sashin koyarwar Yesu an manta dashi. Mun maida hankali kan Allahntakarsa, akan yadda ya cika annabcin zuwan maiceto, gameda mutuwa da kuma tashinsa da kuma zuwansa sama bayan mutuwarsa. Amma yayinda muka duba koyarwar Yesu shi kansa, munga cewa akwai wani babban sashin da ya kamata mu maida hankali kai.

Yesu yazo a wajen karshen tarihin Isra’ilawa na Tsohon Alkawari. Annabawa sun baiyyana abinda suka hango na zuwan hukuncinsu. Yesu yazo yayi bayanin dalilan zuwan wannan hukuncin. Wata irin al’umma ce da ta rarrabu: mutane suna rayuwa bisaga ra’ayinsu, kuma basa kaunar juna. Al’umma ta rarrabu, kowanne bangare ya zama daban. Sakamakon wannan shine yaki tsakanin al’ummai da

kuma Romawa suka sami nasara a nan wanda yasa suka zama shugabanni a wanna sashin. Yawancin koyarwar Yesu ta shafi wadannan alamun.

Yawanci mun fassara koyarwar Yesu ya zuwa irin chanjin ra'ayin karni na goma sha shida. Lokacinda muka ga Yesu yayi gaddama da Farisawa, munga wannan gaddama akan aiki da kuma  bangaskiya. Kuma mun fassara wasikar Manzo Bulus ta wannan hanyar. Munce Yesu da Manzo Bulus basu yadda da shari'anci ba a matsayin hanyar ceto. Yesu, munce, yana nuna rashin ingancin aiki wajen kaimu zuwa sama, sai ya bada tabbacin bangaskiya a madadin haka. Amma yayinda muka duba cigaban bayanin  da Yesu yayi a wannan sashi zamu ga abubuwa daban. Damuwar da Yesu ya samu da shirin Shari'arsu shine cewa addinin da suke amfani da shi ya zama hanyar boyewarsu ce kawai daga bukatar wadansu. Basa bautawa wadansu: wadanda suke a wadansu matsayi na rayuwa, irin kala da kuma bangaskiya. Wannan shine ainihin damuwar.

Wannan daidai ne mubar shirin shari'a mu koma ga bangaskiya, amma idan nan ne muka tsaya kawai  har yanzu bamu tsaya kan abunda Yesu yayi bayani kai ba. Yana bayani kan zuciyar Allah ta al'umma mai kauna, bisaga kewaye da kuma rarrabuwa  mun kawo tsakanin mu da sauran mutane. Yesu yayi Magana kan shari'anci a matsayin wata damuwa da ke hana lura da sauran mutane. Manzo Bulus yayi Magana kan shari'anci a matsayin abinda ke hana hadinkai cikin iyalin ikkilisiya. Wannan shine babban bayanin Bulus yayinda yake Magana kan tsira ta wurin bangaskiya. Baza'a duba bayanan Bulus ba a hanyar yanayin mutane na sashin yamma ba, amma tawurin burin Allah na al'umma.

Yesu ba lallai yana tambayarmu kaucewa tauhidin karya bane zuwa wanda yake daidai bane. Ba wai yana gaya mana kawai bane mu bada gaskiya ga abubuwan dake daidai bane. Ko almajirantarwa tana kan koyon bangaskiya ta daidai bane. Almajira shine wanda ya bi Yesu, wanda ya dauki irin rayuwarsa ta mika kai ga mutane da suke kewaye da shi, jawo su zuwa iyalin Allah tawurin bangaskiya. Almajirantarwa yana kan zumuntarmu da kuma yadda muke rayuwa tare da iyali da kuma al'umma. Zamu iya chanzawa zuwa tauhidin dake daidai gameda bangaskiya amma har yanzu muna tare da Farisawa tawajen abunda Yesu yake Magana a kai.

Dukan abubuwan da Yesu yayi cikin bishara yana gameda lura da mutane: yi musu ziyara, yin kokarin biyan bukatunsu da kuma banbanci, taimakon wadansu a ranar asabas, da kuma koyarwa gameda Basamariya mai kyau. Wannan ya nuna cikakken banbanci tsakanin sabon mulkinsa / na lura da hanyar rayuwar wadansu da kuma irin hanyoyin Farisawa da kuma hanyar tafiyar da mulkin su.

**KARANTA YESU DABAN**

Bisaga tauhidin yammacin duniya yawancin lokaci mu masu banbanci ne. Wannan na nufin muna rarraba abubuwan ruhaniya da sauran abubuwa. Yawancin koyarwar Yesu an maida ita a ruhaniyance, kuma muna amfani da su kawai a hanyar da zamuje sama. Amma sama wani karamin sashi ne na abunda Yesu yayi Magana akai, kuma yayinda yayi maganar sama yayi ta ne musamman kan yadda zamu iya yin rayuwar ka'idodin sama anan duniya. Abunda Yesu ya nanata shine, “Mulkin ka shi zo, da kuma mu aikata nufinka anan duniya kamar yadda yake a sama.”

Wannan shine abunda wa'azin kan dutse yake nufi. A lokacin karni na sha biyar, Augustine, ya maida wa'azin kan dutse a ruhaniyance, domin ya hada shi da sabon chanjin tauhidi dake zuwa cikin ikkilisiya. Bayan Constantine, shugaban Roman Emperor, ya hada wannan kasar da ikkilisiya, ikkilisiya ta fara sake chanza yawancin tauhidin ta zuwaga sabbin hanyoyi. Augustine ya dauka cewa zamu iya cika umurnin Yesu na kaunar makwabtan mu amma kuma a yawancin hanyoyi muna kashe shi da takobi. Yace Yesu yana Magana akan irin halayen mu na ruhaniyar zuciyarmu. Wannan wani babban chanji ne bisaga abinda Yesu ya koyar. Yesu yana Magana kan sasanta al'umma, harma da makiyanmu, a nan duniya.

Koyarwar Yesu tana gaba daya ne. Bai banbanta tsakanin ruhaniya da kuma sauran abubuwa ba. Wannan ya hada abunda Yahudawan Tsohon Alkawari suka fuskanta. Rayuwa daya ce. Bishara ba ruhaniyar irin rayuwar mutane kawai bane. Duka gaba daya ne. Samun chanji na ruhaniya yana kawo samun chanjin rayuwar mutane. A cikin Yesu babu banbanci. Burinsa shine mulkinsa yazo cikin zuciyarmu domin a samu cikakken chanji a zumuntarmu da sauran mutane, wanda a nan zai kawo babban chanji na yadda al'ummai zasu kasance cikin kasashen mu. Nufinsa shine na mulkin ya chanza duniya gaba daya, kamar yadda Ishaya da sauran annabawa suka hanga. Fahimtar wannan zai iya shafar yadda muke karanta abinda Yesu yace.

Tun daga zamanin Magnificat har ya zuwa yanzu, munga wannan cewa “rayuwa daya ce" wanda yake musamman akan bisharar Luka. Luka yayi amfani da zuwan mulkin ga chanjin rayuwa. Yohana mai Baptisma ya nuna bishara a matsayin

rarraba kayanmu da abincin mu da sauran mutane, da kasancewa da hakuri da abunda muke da shi a maimakon zari. Wannan yana bayan rashin jin dadi a Urshalima a wannan lokacin, da kuma irin hanyar rayuwar Yesu da mutuwarsa ainihi ba na kaffara bane, amma kuma ya zama farkon sabuwar rayuwa da kuma sabuwar hanyar yin abubuwa. Wannan sabuwar al'umma, zata chanza duniya dake cikin tashin hankali. Ya fara a masujadar Nazaret. Cikin littafin Ayyukan Manzanni, Luka ya nuna wannan ikkilisiyar mai chanji cikin aiki, kauna da kuma chanjin makwabta zuwa 'yan'uwa, ta ruhaniya da kuma ta sashin dukiya, yayinda bishara da ruhaniya suka sabunta zukatansu.

**AL'UMMA NA NUFIN HADUWAR MUTANE TARE**

Wasu sassa cikin littafin bisharar Luka a dubawar farko na iya nuna cewa kamar hada su tare a wata hanya daban; duk da haka, Luka yana baiyyana sabon mulkin da yake a nan duniya wanda Ishaya yayi annabci, sabon mulki mai tsarki wanda zai sabunta dukan duniya.

Mun ga wannan, a misali, cikin farkon Luka 11 cikin addu'ar Ubangiji, "Mulkinka yazo, a aikata nufinka a duniya kamar yadda ake yi a sama." Wannan jigon bayanin ya hada bayanin Luka na sura 11 da kuma abinda ya biyo baya, a yayin fito-na- fito da Farisawa, Yesu ya gabatar da wannan sabon mulkin da kuma bayani a kan banbancinsa tsakanin shi da al'adun jama'a dake cigaba / na mulkin shedan wanda Farisawa suke amfani da shi kwarai sosai.

"Duk mulkin da ya rabu a kan gaba, zai lalace."Wannan ya gabatar da bayanin Yesu. Urshalima zata fadi a wannan zamanin saboda rabuwar ta. Urshalima tana kamar gonar inabi cikin Ishaya 5, wadda Allah ya kira ya tsarkake, amma kawai suka zama 'yan tawaye kuma suna da ruhohi guda bakwai da masu karfi wanda suka fi karfi kuma suka lalatar da birnin. Tawayen su shine rashin yadda su sha wuya su bautawa wadansu kamar yadda Yesu yayi. Yesu ya kwatanta hanyarsu ta tafiyar da mulkinsu da na sabunta rayuwa da kuma sabon mulki, yayi amfani da wadansu mahimman kalmomi guda biyu: "rarrabuwa" da "taruwa."

Farisawa sun rarrabu. Irin rayuwarsu ta son kai na nufin basu damu da lura da marasa lafiya ba, masu bukata ko kuma masu zunubi. Su sun zama masu wariya kawai, rarraba mutane, wadanda ke ware al'umma yayinda su kansu suna rayuwar jin dadi. Al'umma ta rarrabu tsakanin "masu abun hannu" da kuma "marasa shi", tsakanin jinsi, kala da kuma irin yadda muke, a yayinda dukan bayanan sun rufu: suna kiyaye dukiyarsu. A cikin wannan yanayi na rashin lura da sauran mutane, al'umma zata rabu kuma ta karye a dan karamin layi.

Yawancin koyarwar Yesu tayi bayani ne akan wannan babban damuwar ta karni na farko. Rayuwar Yesu misali ne na akasin wannan mulkin: wanda ya taru. Ya tara masu zunubi, samaritawa da makiyan gafara na ikkilisiya, yi masu ziyara, hadawa da, warkarwa, koyarwa, ciyarwa da taimakon wadanda suke cikin bukata. Nan an

sami cikakkiyar rayuwa ta ‘yanci da kuma chanji a wannan kwanakin. Wannan ‘yanci na Yesu, rashin rarrabuwarsa, da kuma irin rayuwa ta nuna kauna ya zama abunda ya shafi irin wadannan mutanen a wannan lokacin, kamar yadda yake ga masu ra’ayin addini ayau.

Al’adun mu na mutane sun sami kafuwa ta hanyar mutane ne. Wani shugaba yana iya daukar wani da kuma abubuwan da yake dasu masu kyau. Yana rarraba al’umma tsakanin masu goyon baya da marasa goyon bayansa, yana taimakon wadansu da kuma hana wadansu. Yana amfani da kowanne dalili domin yin haka, harda addini, ko kuma rabuwar addini a kungiyoyi. Mutane suna gina manyan runbuna domin jin dadinsu, kuma domin samun bayanan mutane gameda irin kayan da suka sa cikin rayuwarsu, aiyyuka masu nasara, motoci, gidaje da yara, bayan kuma wadansu a kauyukansu ko biranensu suna shan wahala. Irin wannan mulkin dole ya fadi. Yawancin kari, mutanen da suka rasa wannan zasu zama ‘yan tawaye, masu tada hankali da sauransu. Yakin basasa da kuma fadan cikin al’umma zai yaga wannan mulkin ya rarraba shi.

A nan munga a fili yanayin mulkin Yesu da kuma amfanin ikkilisiya a duniya. Mune masu tattarawa, makiyaya, da kuma masu lura da sauran mutane, ko yaya irin al’umma da yanayin kalarsu. Mun ki mu dauki saura ta yanayin matakin kungiyoyi, amma mun karba kuma mun tattara mutane domin bautawa dukan al’ummar mu, domin warkar da cututtukan da kuma sake gyara ramukan da aka samu. Muna nuna alherin Allah, kamar yadda aka nuna mana cikin Kiristi. An nuna bishara tawurin rayuwarmu. Mulkin jinkai, wanda yake tattarawa, zai tsaya. Zai ci nasara a kasashe. Zai tabbatar da wahayin Ishaya. Zai kawar da shaidan daga al’ummar mu.

“Wanda ya tattara yana tare dani.” Wannan shine fuskar ikkilisiya, a sabon mulki.

“Rarrabuwa” yafi yawa a lokacin bangaskiya cikin tsohon alkawari. Cikin Farawa an raba haske da duhu da kuma kasa daga teku. Wannan yayi Magana kan Isra’ilawa na rabuwarsu da sauran al’ummai. An sa rabuwa cikin litattafan tsohon alkawari, tsakanin mai kyau da mara kyau. Yayinda Yesu yazo sun tsammaci irin wannan daga gare shi. Amma ya nuna cewa rabuwa na nufin zuciya mai tsarki, kuma yana nufin munayin abubuwa a hanyar Allah. Ba mun rabu ta yanki bane

daga makiyan mu ba, amma mun rabu ta yadda muke maida martini ga mugunta. Irin rayuwar mu ta nuna kauna wadda zata warkar da makiyanmu.

**Bayyana Gajeren bayanan Yesu**

“Lokacin da ka shirya buki, kada ka gaiyaci abokan ka kadai, amma har da guragu da marasa lafiya…..”

“Yayinda ka gaida mutane a cikin kasuwa, kada ka gaida abokanka. Ka gaida harda marasa bi. Menene banbancin bangaskiyar ka da tasu, idan kana yin kamar yadda suke?”

Wadannan sune gajeran hanyoyin koyarwa. Yesu ba yana Magana kan irin bukin da muke yi ba. A cikin yanayin koyarwar Ibraniyawa, yana amfani da wadannan gajeren darussa domin ya koyadda mu a matsayin kashi na farko domin mu dauki sashin rayuwa da yawa da yake kokarin koyama na wannan duniya; amma zamu fara da abincin mu na musamman, abincin bukukuwa kamar bukin aure, bukin Kirismas da sauransu.

Da farko, bukukuwan mu. Yawanci muna gayyatar mutanen da muke so kusa da mu, sai mu shirya abincinmu mu tsabtace gidan mu. Munaso wadannan bakin suyi cikamako kan abubuwan da muka samu sabbi da irin abincin da mukayi, amma abinda Yesu ke cewa shine mu hada da wadanda ke kewaye da mu. Yana gaya mana mu gayyace su zuwa bukinmu, ya zama kamar sun gaya mana, “Mu lura da makiyanmu da kuma wadanda bama kauna, wadanda ke cikin wahala ko suke cikin bukata, kamar abokan ku da iyalan ku. Ku lura da saura kamar yadda kuke lura da abokanku.” Wannan ba shi kadai bane abunda ya kamata ko abu mai kyau ko kuma abun kauna, amma wannan shine irin shirin karni na farko. Yesu ya fadi gameda Urshalima, “Idan dai kasan abubuwan da suke kawo salama.” Wannan na cikin daya daga cikinsu.

Zamu iya duba yanayin taron Kirismas namu. Mun duba yanayin kasancewar abokan mu, mai yiwuwa mutanen da zasu bamu kyauta. Na tuna da matsuwa ta a Kirismas lokacin da nake yaro karami. Idan kyautar da na karba bata kai wadda na bada tsada ba, daganan sai in damu kwarai. Ko kuma, idan kyautarsu gareni tafi tawa tsada dana basu, sai in inji kunya. Yayinda muka duba kudin da zamu kashe lokacin kirismas, kasha nawa muka kashe a kanmu “yana motsa dukiyar mu”, bayan wadansu na ta shan wahala, shi yasa ba mamaki wasu zasu duba su yi

tambaya, “Wannan shine addinin Kirista?” shin wannan shine abunda mutumin da suka bada gaskiya yayi a lokacin Kirismas ta farko a Baitalami, yayinda ya bar dukan kome yazo gare mu, makiyansa?” Don haka wannan shine zamuyi a lokacin Kirismas: Abinda Yesu yayi.

Daganan munga abunda Yesu yace gameda gaida mutane. Muna gaida abokan mu; Yesu yace zamu gaida wadanda suke kewayen mu. Ba yana maganar gaida mutane kawai bane. Wannan gajerar koyarwa da ake cewa mu dauki wadanda suke wajen kewayen mu kamar yadda zamu dauki mutanen mu, mutanen iyalanmu da abokanmu, hakanan mutanen ikkilisiyar mu. Zamu lura da sauran mutane a kewaye da mu, kamar yadda muke lura da kanmu. Idan ba muyi haka ba, al’umma na iya rabuwa. Idan mukayi haka, al’umma na iya warkewa kuma ya tsaya da karfinsa. Haka nan muna nuna wannan kauna ga makiyan mu da wadanda ke neman suyi mana illa. Wannan shine Yesu yayi kuma muma an kira mu mubi shi a matsayin almajiransa. Duniyar mu tana yadda take yau, ba domin laifin wadansu kawai ba, amma saboda dukanmu gaba daya bamu yarda muyi biyayya kan abubuwa masu sauki da Yesu ya nuna mana.

Koyarwar Yesu masu sauki ne. Muna duba manyan darussa daga gare su, amma suna nan domin mu da makwabtanmu. Martani ga kwabtanmu kamar addini ne. wannan shine yawan abunda Yesu ya koyar. Yayinda muka je masujada sai muka tuna mun bata da wani, ya kamata mu koma wurin wannan mutumin muje mu sasanta abinda mukayi, kafin muje muyi sujada. Wato, yin zamunta da makwabtan a hanyar da ya kamata, ko yaya wannan makwabci yake, maganar sujada ce. Ba muna zuwa wurin Allah don sujadar kanmu ba, tawurin yadda muka dauki da sasanta da sauran mutane, hadi da makiyanmu. Dukan koyarwar Yesu suna kan koyarwar al’umma ne, saboda al’ummar da suka warke kuma suka albarkaci sauran mutane yana cikin zuciyar Allah. Allah ya mika hannunsa ga makiyansa domin su gina sabon al’umma, idan mukayi haka ga sauran mutane, to mu ‘ya’yansa ne.

Anan ne muka san ra’ayin Yesu na bangaskiya. Yace idan bamuyi wannan abubuwan ba, yaya bangaskiyar mu take da banbanci da marasa addini? Yace bangaskiya ba wani abunda muke da shi cikin zuciya bane, ko a yin sujada, ko

kuma a irin kungiyar da muka sa kanmu. Ba yin addu'ar "masu zunubi bane". Hanyar yin rayuwa ba ce: hanyar rayuwar sa. Almajiranci ne; a matsayin masubinsa. Wannan itace bangaskiya.

"Yayinda kake bada kyauta kada ka ba wadanda zasu maido maka wannan kyauta, amma ga wadanda bazasu iya maido da kyautar ba."

Wannan ne ke faruwa bisaga iri yanayin rayuwar mu. Idan wani ya gayyace mu zuwa buki, muna tunanin ya kamata ne mu kawo wani abu. Ba wai suna bukatarsa bane, amma idan bamu yi haka ba, mutane na iya kinmu. Muna baiwa mutane domin kanmu, ga wadanda muke sauraron su maida martani. Muna ganin wannan a maaikatu da dangantakar mutane. Wannan ya nuna cewa, yawan abunda muke bayarwa shine ke kawo mana damuwar mu a duniya yau; duk da haka muna kokarin sa wadannan damuwar ga wadansu mutanen. Yayinda damuwar wadansu na ciki, zamu farad a rayuwarmu, da abinda Yesu ya fada mana muyi. Bayanin Yesu ba yana kan Romawa bane, ko kokarin addini bad a 'yan ta'adda ba; yana Magana akan mune, mutanen Allah, abinda ya kmaata muyi, domin muna da haske da kuma maganin abun, idan mukayi amfani da shi.

Duniya na samun warkarwa idan muka bayar a kyauta ga wadanda suke da bukata, ba ga kanmu ba. Wadannan gajejjeran koyarwar na Yesu sune maganin rarrabuwar al'ummar mu, nuna yadda sabon mulkinsa yazo cikin tsakanin mu, wanda Yesu ya bamu a fili, a yarai mai sauki.

Muna bukatar mu kama hanyarmu zuwa al'umma, wanda ke nufin mu sa wadansu cikin rayuwarmu da kuma dukiyarmu. Ba zai zama rayuwa mai sauki da farko ba. Hadawa da wasu mutane yana da wahala; bamu saba da wannan ba. Yawanci mutane ne masu wahala. Hakika suna da banbanci da mu sosai. Banbanci yana da kalubale. Muna gani laifinsu fiye da yadda muke ganin namu laifin, amma abun shine, bisharar duk tana kan kauna ne, kuma kauna itace koyon yadda zamu maida kanmu ga sauran mutane, mu karbe su mu kuma taimake su, mu kuma kyale kanmu su taimake mu. Yesu yazo cikin rayuwarmu da abokansa. Cike take gaba daya. Bazamu iya tafiya da shi batare da tafiya da al'ummar sa ba. Zamuyi girma cikin Yesu idan mukayi girma tare da sauran mutane duka.

**BISHARA MAI BANMAMAKI DA UBANGIJI**

A cikin karni na farko, mutane da yawa ciki Isra'ila suna sauraron maiceto wanda zai zo yayi masu ramako. Zai yi makiyansu horo da kuma ya maido wa Isra'ila daukakarsu, kamar yadda take a lokacin sarki Dauda. Zai zama maiceto kamar sarki Dauda, wanda zai maida makiyansu shan wahala. A karshen duka zai tsaida makiyansu daga bata musu rai.

Wannan shine irin begen mu na addini; hanyar da muke ganin Allah. Cikin dukan addinan mutanen duniya muna ganin Allah a matsayin wanda ke zuwa domin ya albarkace mu, ya kuma kara mu, ya tanada mana lafiya, da dukiya da jin dadin rayuwa, kuma ya hukunta makiyanmu. Amma wannan ba shine irin Allahntakar da Yesu ya nuna mana ba lokacin da yazo. Hakika, ya warkar da mu, amma rayuwar sa ce da kuma rayuwar al'ummarsa ne yakeso mu gani, mubi da kuma muyi. Wannan itace warkarwa. Wannan shine kasancewa kamar shi.

Koyarwar Yesu abun kunya ce sosai a lokacinsa. Ta sha bambam da dukan tunanin mutane. Yana sharhi kan dukan mutanensa da kuma kasarsa, ba makiya ba. Yace albarkace mu sha wahala, ba muyi daidai a tunanin mutane ba. Abin ban mamaki ne yayinda wani yace, "Allah ya albarkace ka." Yayinda muka duba dukan kome cikin bishara wadda Yesu ya kira albarka, zamu gane cewa yana ma'anar wani abu da wanda muke nufi bane gaba daya. Koyarwarsa cin amanar kasa ce a fuskar mutanen sa.

Irin tunanin mu na mutane gameda Allah shine wanda yake abu mai hadari cikin abubuwan dake duniya. Saboda kowa yana ganin Allah ta irin nasa tunani, a matsayin wanda zai albarkace su kuma ya hori makiyan su shi yasa bazamu so rayuwar al'umma da Yesu yayi Magana akai ba. Bazamu iya zuwa cikin mulkinsa ba cike da zuciyarmu ba anan duniya yayinda irin wannan wahayin na yadda Allah yake yana cikin mu.

Irin fahimin mu gameda Allah yana kaimu ga rarrabuwa, tsatstsaguwa, tashin hankali, rashin hada kai da wadansu, da kuma yanayi. Yesu bai zo domin ya inganta irin wannan bangaskiya cikin rayuwarmu ba.

Addini zai ingiza laifi, ko kuma “ya kawo sanin abu mai kyau da mugunta” cikin tunanin mu. Laifin Adamu na irin rayuwar sonkansa da martanin sa ga Allah kan kaunar Allah mai kyau ce ta, wannan ya bautar da shi kuma ya kauda shi daga fuskar Allah da ya boye. Allah bai kori Adamu ba daga gabansa kuma kaunar Allah bata chanza ba a gameda Adamu, ya kiyaye Adamu daga wannan yanayi da yake a hannun shedan.

Wannan laifi shiri Shedan domin ya bautar da mutum, kamar yadda aka rubuta cikin Romawa 7. Hakanan kuma shirin shedan ne yayi amfani da addini domin ya kawo mana gaba tsakanin mu da juna. Ya kawo tashin hankali kala kala, yayinda muke kokarin mu ‘yantar da kanmu da laifi tawurin dora laifi ga wadansu. Farisawa sunyi haka kuma Shawulu na Tarsus ya samu wannan bishewar, duk wannan lokacin yana ganin yanayin nufin Allah ne. wannan ya nuna karyewar dangantaka, ikkilisiya ta rabu, da kuma cikin hanyoyin mai Tsanani. Wannan yanayi ne farfaganda, wanda yake nunawa duk lokacin da muke da damuwa. Sasancin Allah cikin Kiristi ya maido da tunaninmu, wanda ya taimake mu muyi kauna, a madadin muyiwa marasa bi shari’a.

Yesu yana da wahalar fahimtarsa a matsayin maiceto. Shi abin tsoro ne ga birane da kuma ga mutane. Bazai iya chanza irin yanayin al’ummar mu da ta rarrabu ba. irin wannan maiceto dole ya tafi. Dole ne a kashe shi. Nayi tunanin Yesu zai sami irin karbuwa idan ya dawo yau. Takobin da ya kawo domin shine da masubinsa. Me Yesu yace gameda irin maida martanin mu? Yace maida martanin mu ya zama na kaunar makiyanmu, inganta salama, biyan bukatunsu, kuma idan ya kai ga mutuwa domin bishara. Yesu yazo ya nuna mana wani Allah daban: Allah na gaskiya.

**SHUGABANCI NA MULKIN SAMA**

Yesu bai taba daga hannu akan mutane makiyan Allah. Yaki ya kira wuta akan kauyuka wanda suka ki shi, ya warkar da kunnen daya daga cikin wadanda suka kama shi, ya kyale Barabbas dan ta'adda ya tafi 'yantacce kuma ya gafartawa wadanda suka gicciye shi. Muna da matsala a yau ta wata hanyar matsala ce mai kyau: Allah ba yana kaunarmu ka dai ba, amma yana kaunar makiyanmu kuma yana fatan da zasu zo su tuba su sami ceto. Idan da Allah ba haka yake ba, da muma bazama samu daga cikin yanayinsa mai kyau ba. don haka ya kamata mu tuna da wannan yayinda wadansu suka cuce mu, kuma mu kaunace su. Suna bukatar alheri domin chanji suma.

Wannan shine kome akan wa'azin kan dutse yake. Sukayi tunanin "Maiceto zai cece su daga Romawa". Amma Yesu yace, "Ku masu albarka ne yayinda aka tsananta muku." Wannan shine muke zuwa ikkilisiya ranar lahadi muji? Wannan maiceton hakika baya yin aikinsa. Wannan laifi ne.

"Idan wani ya kira ka ka dauki kayansa mil daya, ka dauka zuwa mil biyu." Wannan yayi daidai da dokar Romawa, wadanda duk lokacin da sojan Roma yake bukatar taimako a tafiyarsa zai iya baiwa kowa a hanya umurni ya taimake shi. Wannan mutumin bisaga dokar Roma dole zai dauki kayan wannan sojan zuwa mil daya. Ga Yahudawa kuma, wannan dokar sabo ne. "Me yasa zamu taimaki masu bata masujada, masu bautar gumaka, da kuma masu kashe kananan yara, wadanda suke tsara dokokin da ba na Allah ba a al'umma?"

Sojojin Roma marasa imani ne. Suna cikin ainihin masu watsi da 'yancin mutane da kuma 'yan ta'adda na wancan zamanin. Hakika maiceto zai zo, kuma zai yi aminci bisan su. Muna da wani irin tunani gameda aminci, musamman irin amincin mu, musamman yayinda yazo gameda shan wahala. Amma Yesu ya kalli aminci daban da mu. Wannan shine damuwar wa'azinsa. "Ka dauki kayansa zuwa mil biyu" Yesu yace. "Yaya, zamu taimaki wannan soja daukar kayan yakinsa zuwa kauye na gaba, domin yaje yayi ta'addanci ga 'yan'uwanmu da ke zama a wannan kauye?" Na'am.

“Idan wani yanason rigarku, ku bashi harda taguwarku ma.” “Ku baiwa duk wanda ya roka, kuma kada ku bada rance.” “Ku kaunaci makiyanku.” “Kuyi abu mai kyau ga wadanda suke tsananta muku. Ku albarkace su.” Kada ku ki (da tashin hankali) mugu.”

Ha, yaya zamuyi da duk wadannan? Kauna a hanyar Yahudawa  ba halin zuciya ne kadai ba. Tana nufin lura da bukatun sauran mutane. Abinda muke yi ne. Bazamu yarda da ra’ayin Augustine ba wanda yace Yesu ba yana nufin abinda ya fada ba anan, amma yana maganar gafarar cikin zuciya ga makiyanmu. Yesu na nufin wannan, kuma ya nuna abinda yake nufi da rayuwarsa. Ya fada mana a fili, “Ku dauki gicciyenku ku biyo ni”. Babu wani irin addinin Kirista fiye da wannan.

Me yasa bamu yarda da wannan ba?

1. Mai yiwuwa saboda son kayan duniyar mune. Mun zama masu ra’ayin kayan duniya cikin wannan hanyar rayuwar mu, kuma muna daukarsu da bada mahimmanci ba. “Daidai ne lura da kayan da muke dasu.” Wannan shine dan hayar al’ummar mu ta yau. Amma Yesu yace, “Kada mu zama masu kyashi, saboda rayuwar mutum bata kunshi dukiyarsa ba.” Duk da haka zamu kai kara domin dukiyar mu yau, domin sasancin rabuwar aure, domin namu sashin dukiyar yayinda wanda muke kauna ya mutu, da kuma dukan sauran kome. Yaya wannan zai tafi daidai da irin rayuwar da Yesu yayi?
2. Mai yiwuwa domin mun bada gaskiyar cewa “sakayyar ido, ido ne” irin hukuncin da zai kiyaye al’ummar mu. “Muna yin wannan domin mu tabbatar da doka a kasar mu.” Me yasa Yesu bai yi haka ba a lokacin? Me yasa yaki “sakayyar ido, ido ne dakuma hakori domin hakori?” Me yasa yace, “Kuyi gafara kamar yadda Ubanku na sama yayi gafara”? Me yasa koyarwarsa kan gafara ya zama da matsala domin haka ya bada tsoso ga irin tunanin almajiran? Me yasa yaki irin wannan shari’ar, saboda shari’ar aminci? Domin shari’a mara aminci a karshe bata yin aiki nagari, kuma shari’ar aminci tana zuwa daga zuciyar Allah da hanyarsa ne. Allah yazo tawurin Kiristi domin ya nuna mana yadda yake.

Wannan shari’a cikin aminci tana kawo sasanci. Yesu annan yana Magana gameda maido da zumunta. “Akwai wani abu mafi mahimmanci da kayanku da kuma har da rayuwarku a wannan duniyar, kuma wannan shine maido da zumunci, kuma wannan shi yasa na mika rayuwa ta da farinciki domin sasanci da kuma zumunci tsakanin Allah da mutum. Ku biyo ni.” Yesu yana nuna mana yadda zamu iyayin sasanci da makiyanmu a hanyarsa. Akwai wani abu mafi mahimmanci da zaman mutum kadai shine zumunta da makiyanmu. Su mutane ne: mu kaunace su fiye da yadda muke kaunar rayuwarmu. Wannan shine Allah yayi.

Wannan itace babbar Magana a rayuwar mu. Dukan mulkin Allah yana gameda sasanci. Wannan shine ake nufi zama gishiri da kuma haske. Tana nufin kaunar makiyanmu yayinda muke shan wahala a hannunsu. “Uba ka gafarta musu, domin basu san abinda sukeyi ba.” Yayinda suka zalince mu, daganan mu basu kuma mu taimake su. Wannan shine wa’azin bishara. Wa’azi shine kiran kan Yesu Ubangiji, wanda yake yin bangaskiya ta hanyarsa.

“Ku dubi dai tsuntsaye. Ai, ba sa shuka, ba sa girbi, ba sa kuma Tarawa a runbuna, amma kuwa Ubanku na sama na ci da su. Ashe, ko baku fi martaba nesa ba?”

An fadi wannan ta hanyar bin Yesu da kuma aikata abinda yace. Yin biyayya. Allah zai lura da mu. Ba zamu yi rayuwa bisaga yadda al’ummar mu tace mana muyi ba. Ba zamu dauki rayuwarmu yadda muke so ba. Ba sai mun ajiye dukiyarmu sai nan gaba ba, yin tunanin kanmu ba; zamu iya lura da wadansu da basu da begen nan gaba. Zamu iya kaunar makiyanmu, hakanan Allah zai yi kuma aiwatar da kaunarsa gare mu da hannu sake. Ba lallai kowanne lokaci zai zama da dadi gare mu ba, amma za’a dinga samun yawan kauna, zumunta da cikakkiyar rayuwa.

“Kada ku damu tumaki kanana, domin jin dadin Ubanku ne ya baku mulkinsa.”

Allah na jiran duniya ta koya da kuma muma, mutanensa, mu nuna da kuma jagoranci hanyar, ta wurin alherinsa mai ban mamaki. Idan muka dauki gaskiyar kamar yadda Yesu ya nuna mana, zamuga yadda Allah mai jumriyar wahala yake tare da halitarsa; dogon lokacin da ya jira mu. Halinsa da hanyoyinsa suna da banbanci da wadanda muke tunani. Faduwar mutum tana cikinmu sosai da kuma cikin al’adun mu.

Wa’azin Yesu na kan dutse shine koyarwarsa ta al’ummarsa. Wannan itace hanyar da zamu rayu yayinda muka bi Yesu cikin gina al’umma da kuma mu kawo mulkinsa a nan duniya kamar yadda yake a sama. Wannan itace hanya. Wannan itace hanyar dake da ban da duhu. Allah bazai shawo kan mugunta da amfani da hanyoyinsa ba. zai tsaya kan hanyoyinsa da halinsa, wanda ya nuna mana cikin Yesu. Allah ya kasance Allah kome makiyi yayi, kuma za’a ci nasararsa kurum tawurin alheri. Wannan shine ya maida hanyarsa ta zama ‘mai wuya’ a idanuwan duniya. Wannan shike bukatar hakuri da ke kawo irin halayensa cikinmu, yanayinsa, chanza mu zuwaga irin kamanninsa na gaskiya.

Yayinda muka ce mune “masubin hanya”, ba muna nufin hanyar zuwa sama kawai bane, amma hanyar rayuwa a nan duniya:Yesu hanyar rayuwa. Yawanci muna cewa Yesu yasha wahala dominmu a matsayin maiceto, da kuma shan wuya yanzu ya kare, saboda haka bamu bi hanyar rayuwarsa ba: domin shi ne a matsayin maiceto. Amma ba abinda Yesu yace ba kenan. Kamar yadda yake don Kiristi, haka kuma domin jikinsa. Mu daya ne cikin shanwuya, ta yanayi, cikin shugabanci da kuma cikin rayuwa kuma muna rabawa cikin cikakken mulkinsa.

Shan wahala wani darasi ne mai ban mamaki kuma yawancin ra’ayin mu nashi ba na hanyar maikyau bace. Dauki Ishaya 53 a misali, wanda ya bayyana shan wuyar Kiristi a fili. Mutane “suka raina shi, suka ki shi, Ubangiji ya auko da hukuncinsa kansa.” Suka raina wahalarsa. Mu mabiyan wannan Kiristin ne yayinda muka ganshi cikin shan wahala don wadansu kuma ya dauki wadannan mutane zuwa cikin zuciyarmu.  Ishaya 53 wannan kalubale ne gare mu a matsayin a dangantaka da duniyar wahala. Idan muka tsaya gefenta, mun tsaya gefen Kiristi ken an.

**NASARA KAN MAKIYANMU**

Ina zamu fara da wannan? Tsohon alkawari yana cike da tashin hankali. Tashin hankali ya zama irin al'adar mutane tun faduwar mutum. Allah yayi aiki kan wannan, yayinda yake ba mutanensa wakilin sabon mulki da yake zuwa, lokacin da zai bayyana tawurin Dansa, ya nuna mana hanyarsa kuma ya bamu sabuwar zuciya.

Tsohon alkawari na cike da alamu da kuma alamun al'adun wannan lokacin, kuma dukan wadannan anyi amfani dasu domin yin maganar zuwan mulkin Allah; amma hanyar da wannan alamu da sauransu zasu cika ya zama a boye kuma wani abun ban mamaki domin irin karfin zuciyarmu. Idan da akwai wani abu daya da tarihi ya nuna shine rashin iyawarmu ta nuna yadda Allah zai cika annabcin mulkinsa; duk da haka muna da gaba gadi cikin hangen mu, wani lokacin mukan sa su kamin zumuntar mu da wadanda suke da wani ra'ayi daban.

"Zaka mallake su da sandan karfe, zaka farfashe su kamar tukunyar yumbu." Zabura 2:9

Zamu iya kiran aya bayan wannan ayar ta tashin hankali dake cikin tsohon alkawali. Allah yayi alkawari a fili cewa zai rinjayi makiyan Isra'ila. Yace zai yi haka da cikakken ra'ayi. Wadannan alkawuran suna cike kuma hadi da annabcin wakar baka, amma sun rabu zuwa abu biyu: 1. Allah zai rinjayi dukan makiyanmu. 2. Zai yi wannan da cikakken nasara. Wannan bi da zata zama cikakkiya, na karshe da harabada. Bari mu kara na uku: 3. Wannan zai kawo kuma zai abunta dukan halittar Allah, hadi da dukan duniya.

Daniyel ya sa wannan babban wahayi na zuwan mulkin. Cikin sura ta biyu munga wata alama mai wakiltar daular mutane da ta sha Tsanani. Wani dutse yazo daga sama ya ruguza wannan alamar zuwa kura, wadda aka hura ta zuwa wani gefe. Sai dutsen daga nan ya cika kuma ya sabunta dukan duniya. Mutane da yawa a Isra'ila suna shirye kuma suna jira zuwan irin wannan maiceto yazo ya hallakar da makiyansu. Daniyel har ya bada ranar da kuma wurin: karni na farko na Palasdinawa.

Abinda ya ba Isra'ila girgizar zuci shine domin suma suna cikin sashin faduwar Adamu, kamar yadda Romawa 7 ta bayyana, suma suna cikin sashin wannan alamar. Suma makiyan Allah ne. Kah! Wannan ya zama wani babban abin mamaki: "Ba abinda ya shiga cikin ciki bane ke kazantar da mutum ba, amma abinda ke fita daga cikin zuciya, wannan shine ke kazantar da mutum." Yesu yace suma zasu iya sa hannu cikin Gehenna, wuri domin "Gog da kuma Magog", wata alama da ta nuna makiyan Allah. "Duba, bama son jin wannan, Yesu. Kayi aikin da muke tunani kawai."

Daga Yesu ya bayar da labarai domin ya bayyana gameda mulkinsa da yadda zai zo. A misalin mai shuka, koma wacce irin kasa mara kyau ce, bayanin a cikin kowanne yanayi yana gameda son kai ne. su ba sa son bautawa makiyansu ko kadan. Wannan mulkin yana shiryawa ya zama wani abu ne daban da basuyi tunani ba.  cikin misalin kwayar mastad daya biyo, tsuntsayen, wadanda suka nuna alamar makiyan (cikin al'adarsu ana amfani da tsuntsaye ne domin nuna alamar makiya kuma wadannan tsuntsayen sune makiyan da suka dauki kwayar hatsin cikin misali na farko), yanzu sune suke hutawa a karkashin reshen ikkilisiya. Wato, cikin mulkinsa, mutanen sa suna lura da makiyansu. Wani babban mahimmin abu ne wanda ya juya da kuma babbar bacin rai.

Babbar matsalar, wadda har yanzu muka kasa rikewa a lokacin mu, shine Allah zai ci babbar nasararsa, ba tawurin hallakar da makiyanmu ba, amma  ta wurin yin sasancinmu. Zai rarraba banbancin dake tsakaninmu (cikin tsohuwar zuciyar mu) kuma ya kawo mu tare cikin sabuwar halitta. Yayinda ya yaga wannan alamar kasa, yana keta zuciyar makiyanmu. Wannan kiyayyar makiyi ce, ba na jiki da jini ba. A bisa kan gicciye, Yesu ya hallakar da kiyayya tsakanin mu da sauran mutane. Wannan ya sa mu kan hanyar sasanci da kuma yin salama a matsayin masubinsa: "Masu albarka ne masu salama, gama wadannan za'a kira su 'ya'yan Allah."

Wannan irin sabon mulki ne, al'umma, sasanci, dake zuwa yayi mulki cikin zukatanmu, wanda key age irin ikokin  da ke cikin yanayinmu da kuma kasashen mu, da kuma sake gina mu cikin kamannin Kiristi. Wannan shine wahayin Daniyel, ya kawo rayuwa cikin bishara. Wannan shine bishara: hanyar

da Allah yake ceto kuma yake sabunta duniya, wanda shine shirinsa, ba ya cece mu kawai ba.

Wannan babban murdawar cikin bishara itace Allah yazo cikin Kiristi kuma ya dauki ruguza doka da kansa, domin ya fanshe mu daga makiyinmu na gaskiya, daga zangon shedan. Ya zama ruguzajje kamar hoda, tawurin tashin hankalin da mu da makiyanmu muka yi masa. Ya dauki zunubanmu tawurin hallaka shi da yayi. Ya hada hannu da mu duka kuma ya zama wannan alamar da ke ciken Daniyel wadda aka ruguza, kuma haka ne yadda ya ruguza kiyayyarmu. Allah ya kyale kansa a ruguza tawurin Kiristi, tawurin tsananinmu, zunubi da tashin hankali, daga nan ya iya yin gafararsa kuma ya karya ikonsa (Ishaya 53:10). Wannan "ruguzawar" Yesu ya chanza ta zuwaga alamar  bishara ta mika kai ga sasanci, wanda ya kamata mu koya a matsayin masubinsa (Ruya ta Yohana 2:26-27).

Domin haka mun sake gani a fili, kada mu zama masu tuhumar makiyanmu, masu zunubi, kamar yadda Farisawa suka tuhumi matar da aka kama cikin yin zina, amma zamu zama bayinsu, kamar yadda Yesu ya bauta mana. Mune muka sa kanmu tsakanin masu zunubi da kuma masu tuhuma kuma mu taimake su, muyi musu jagora zuwa ga alherin Allah da kuma cetonsa. Wannan shine sabuntawa, wanda Allah cikin Kiristi ya kawo salama cikin zukatanmu kuma ya maida mu 'yan aikan salama ga wadansu. Zamu yi kauna, warkar, yi gafara, lura da wasu, bautawa kuma mu jawo makiyanmu, kamar yadda Allah yayi mana.

Sandan karfe (Zabura 2) na nuna alamar cikakkiyar nasara. Ya mulki makiyanmu tawurin sasanci. Kamar yadda manzo Bulus yace, "Ya maida duka Yahudawa da al'ummai (makiyan Isra'ilawa) daya tawurin gicciye, karya katangar tsakiya da rabuwa." Wani babban takaici kenan cikin kwanakin Manzo Bulus! Shugaba na Farisawa, ya tafi kan makiya kamar haka, yana kawo mu tare a matsayi daya. Bulus ma dole ya tafi."

Wani abun mamaki na annabcin zuwan maiceto cikin Zabura 2, shine a cikin al'adar Ibraniyanci, yayinda tukunyar mai yin tukwane suka farfashe zuwa kasa, an maida kasar zuwa wani siminti mai karfi, wanda akayi amfani das hi

domin rike duwatsu tare a sabbin gidajen su. Yesu ya kasance wannan kasar kuma tawurin ruhunsa, kaunarsa ta gicciye mai karfi kwarai ya zama abinda ya rikewa tawurin wanda makiya masu al'adu da yawa suka sami sansanci, aka hadasu da kuma gina su zuwa sabon gida cikin Ubangiji.

Saboda kaunar sa, Allah ya ragargaje makiyansa yayi da kansa cikin Kiristi da kumahaka yayi ceto, ya hallakar da makiyan Isra'ila da abokanta, ya sasanta mu tare cikin jiki daya kuma ya gina wani sabuwar halitar salama. Tawurin wannan ya dauki nasara gaba daya kan Shedan a hanyar da Allah na gaskiya ne zai iya yi. Yayi wannan ba tare da bin wata hanya ta shedan ba. A lokacin yin wannan ya gina wata al'umma wadda ba zata hallaku ba kuma ya sabunta duniya. Me zamuce ga wannan? Ba mu da isashshen yabo da zamu yi yadda ya kamata ga wannan. Ya kira mu mubi bisa wannan matakin da ya aiwatar.

Muna bukatar mu lura yadda muke fassara maganar Allah, kamin mubi irin namu tunani. Da farko yi tambaya, yaya Allah yake kama, menene ya nuna mana cikin Yesu? Yesu cikin bisharun nan, yana yadda muka fassara sauran maganar Allah, domin idan mun ganshi, mun ga Uban kenan. Allah na kiranmu mu bautawa makiyanmu, ba mu kira domin hallakarsu ba. wannan ne shirinsa na sabuntawa. Yayinda mukaso mu hallakar dasu, ko kuma muka manta dasu ba mu taimake su ba, zamu zama kamarsu amadadin zama kamar Allah. Ya kamata mubi hanyarsa, kamar yadda take cikin Kiristi.

**BABBAN ABIN MAMAKI NA DUKA**

Duka yana cikin sashin wani babban abin mamaki: wanda Allah zai yi kan makiyanmu yafi karfinsu tawurin sasanta su gare shi kuma ya kira mu muyi aiki cikin wannan sasancin, harma wajen makiyanmu. Wannan ra'ayin na Allah ya chanza kome gameda yadda muke rayuwa da kuma yadda muke tafiyadda sauran mutane, musamman wadanda suka ki yarda da mu.

Babban abun mamaki a tarihin rayuwar mu shine akarshe mu gano yaya Allah yake kamada, abinda addinanmu basu baiyyana ba kenan, kan irin yanayinsa na gaskiya. Wata babbar abun ban mamaki shine gano cewa yadda Allah mai iko duka yayi yaki da makiyansa. Ishaya yace Allah ya duba amma babu wani mutum da zai yi taimako, domin haka hannunsa ya kawo ceto. Zai shirya a matsayin mutumin yaki kuma ya tafi filin daga da kuma kayan bangaskiya da kuma bel na gaskiya. Yana zuwa wurin Isra'ila domin yaki da makiyanmu.

Wannan shine littafin tarihi ya rubuta. Ta wurin juya Kalmar da wata, wannan na nufin bayyanawa. Menene ake bayyanawa? Abun mamakin! Yadda Allah ke yin yakinsa. Hanyoyin da zai tabbatar da alkawuransa. Yadda zai dauki ikon wannan duniya da ta fadi da kuma ya zuba albarkunsa kan dukan kasashe kuma ya sabunta kasarmu gaba daya. Wannan ba shine irin bisharar mutum daya da muka saba da ita ba a 'yan kwanakinnan. Wannan bishara ce ta al'umma, tawurin da Allah zai tafida gyare gyarensa na dukan duniya.

Cikin Ishaya 45, Allah ya bayyana kalmarsa akan masu bautar gumaka na duniya. Ya bayyana dokokinsa akan duk sarakuna na duniya. Allah zai zo ya jagoranci kasashen nan. Zai ci nasara sosai kuma zai kawar da duk makiyin wannan kasar. Zai dauki mulki bisan dukan mulkoki. "Kamar yadda nake rayuwa inji Ubangiji, gare ni dukan kowacce gwiwa zata duka da kuma kowanne harshe zai bada shaida."Amma babban abun banmamaki shine yadda yake yaki, yadda zai je cikin yaki da sarakuna da kasashe da kuma ya cika ikonsa na mulki akan rayuwar mutane, al'adunsu da gwamnatoci.

Duba shawulu na Tarsus da kuma ban mamakin daya samu. Yana ta kokarin gyara duniya ta zama da kyau, jifan wadannan matan da aka kama suna zina da

sabo, kashe masubi, yin yaki da makiyan rashin gaskiya da masara bin Allah, aiwatar da dokokin Allah masu kyau, daganan kamar wasa zuciyarshi ta chanza. Wannan zai iya zama abu maiwuya a dauka. Yesu ya bayyana ga Shawulu yace masa wannan ba ita bace hanyar yin abubuwa, kuma ya nunawa Shawulu a maimako zai sha wuya domin mulkin Allah.

Wacce irin tafiya ce Bulus yayi kamin yayi wakarsa  dake cikin Filibiyawa 2: wani babban littafi. Allah shine kalma, zai iya zama jariri ba tare da daki ba,  an tuhume shi da zama dan zina, ya zama dan gudun hijira a Masar, kafinta karami a Nazaret, ya dauki tawul a matsayin yaron gida domin ya wanke kafafunmu, aka hallakashi saboda rashin aminci, kuma tawurin mutuwarsa ne a matsayin bawa a kasar Roma yaci nasara da makiyansa. Allah zai yi yaki, amma ba tawurin kashe makiyansa ba, amma tawurin mutuwa domin su kuma da bauta musu. Wannan wani abun ban mamaki ne ga irin namu tunani. Yana da banbanci da dukan al'adunmu kan yin yaki. A wurin Yesu ne kawai  da kuma bishara zamu iya ganin wannan. Irin wannan kaskanci daga mutum daya daga sama, yayi banbanci da irin al'adunmu na mutane, wannan itace babbar abun ban mamaki na duka.

Wannan shi yasa aka sawa littafin Ruya ta Yohana wannan sunan. Ya bayyana yadda Allah cika alkawarinsa na mulkin duniya ya kasance. Ya fara da gicciye kuma ya bayyana a ikkilisiyarsa, wadda ta dauki ruhu na ciki daya. Yohana yaji murya tana cewa, "Zakin kabilar Yahuda ya baiyyana", kuma da ya juya ya ga dan rago da aka yanka. To shi zakin dan rago ne? wannan itace wakar: Dan ragon Allah. Allah yazo a matsayin  Dan rago domin ya yaki makiyansa.

Kuskure ne duba Yesu cikin daukakarsa kuma kuyi tunanin halinsa ko hanyar shugabancinsa ta chanza. Muna tunanin wannan domin mu kirkiro wani abun siyasa "Yesu" domin muyi yaki da makiyanmu. Kamar yadda wani aboki yace, "Dan ragon da aka yanka ne yake mulki duniya da kuma wannan labari ne mai dadi ga sauran mutane." Ko mary  ceta fadi haka? Wannan mahimmancin bayanan Yesu ne.

Dan ragon shine babban alama cikin Ruya ta Yohana, inda aka maimaita shi sau 29. Akwai alamun Yesu a yaki, amma wannan ya nuna "raunin" Allah shine

karfi da nasarar sa. Yana da karfi wurin yaki, amma da gaskiya, da aminci, jinkai da kauna. Ya taka zanen matsarar giya ta fushin Allah, amma kamar yadda aka bayyana a hoton ikkilisiya yayi wannan tawurin mutuwarsa “a wajen birni” ta hake yaci nasara da mutuwar makiyinsa da kuma farfado da kasashe (Ishaya 25-27, 63). Ya dauki kofi ya kuma shaida da yakin mu na Armageddon, ta hannun wannan dabbobin guda biyu na cikin Ruya ta Yohana: Urshalima da Roma. Dukan abind Yesu yace gameda hallakar masujada haka kuma ya aiwatar a matsayin masujadar Allah. Yana da takobi dake fitowa daga bakinsa, wadda yake  hallaka makiyansa, amma wannan na nuna Kalmar bishara wadda ke fita daga kasashe, tana sasanta duniya. Haka Allah yake yakinsa.

Wahayi na nuna daukar ramako na Allah da kuma hukuncinsa, amma hukuncinsa ba yana bayyanuwa bane ta hanyar tashinhankali ba, ta wurin tashin hankalin mutum ya dawo masa. Wadanda suka kashe dan ragon da yin shahadarsa suka zama sun shawu cikin jinin su. An bada su ga hanyoyinsu, suka rasa dukan tunani da kai domin hallakar kai. Allah ya kyale mugaye su hallakar da junansu. Hanyar mugaye tana da hallakarwa. Don haka cikin dukan Tsohon Alkawari annabawa da kuma karni 70 AD, hallakarwar Urshalima, da haka kuma kome zai dinga kasancewa da makiyan Allah: wadanda basu tuba daga tashin hankali ba zasu hallaka kansu. Kuma Allah baya murna da ita.

Alamar yaki tana nuna akida da kuma haduwar shari’a. Allah yakan shiga da kuma ya kada shedan tawurin  Kiristi da kuma gicciyensa. A faraway ta 1 munga irin halin yakinsa. Wato zabi ne, tsakanin haske da duhu. “Nasa gaban ku raid a mutuwa, ku zabi rai.” A wadansu bayanai na zamanin da alloli ne sukayi ainihin yakin, wanda yayi daidai da tashin hankalin  al’ummai. Amma Allah madaukaki ne kuma babu wani hannu da zai daure hannunsa. Yana yakin mugunta da abu mai kyau.

Kiristi dan rago shine shaidar da kuma hikima da kuma hanya: hanyar yin nasara bisa kan makiyansa da namu, da kuma kan bakincikin dake zuciyarmu. Makiyin da za’a kauda yana cikin mu ne. muna yaki da makaman bayar da kai, bautawa, salama da kuma sasanci.

**IKKILISIYA MAI SASANCI**

Sasancin akin Allah yana cikin Kiristi kuma yaci gaba a ciki da wajen ikkilisiya. Bulus da gana da Kiristi bawa mai sasanci/ wahala tana cikin dukan wasikunsa, ba domin Bulus yayi rayuwa a lokacin shan wuya ba, amma domin haka mulkin Allah yake zuwa kuma ya yadu a cikin kasashe. Wani babban aikin da Kiristi yayi shine na sasanta kansa da mika kai domin ya cika kowanne aiki na ikkilisiya cikin duniya.

A nan munga abubuwa biyu:

1. Yadda ikkilisiya take. Ba mu bane shugabanni, amma bayi da zasu jawo da kuma sabunta zukata, rayuka da al'adu kamar yadda Kiristi yayi a kan gicciye. Mu sarakuna da priestoci na Allah, amma ga duniya mu bayi ne, wakilan mulkin sama, muna nunawa ga al'umma nagari, sasanci, bautar rayuwa. Wannan itace irin kamannin Allah cikin Kiristi hakanan kuma muma wannan kamannin mu ne. Haka mulkin Allah ke zuwa yayi mulki a duniya, ba kamar sauran mulki bad a suke zuwa da karfi, su sarrafa hanyarsu ta kowacce hanya ta duniya.
2. Manufar Allah ce a sasanta dukan kome da ke halittarsa zuwa Kiristi, bay a hallakasu ba. wannan shine dagawar mulkin Kiristi, har sai "dukan kome sun zama sabbin."

"Duk wannan kuwa shiri ne, domin a cikar lokaci a harhada dukan abubuwa ta wurin Almasihu, wato abubuwan da suke sama, da abubuwan da suke a kasa."

Afisawa 1:10

Domin cikar lokaci na nufin lokacin bishara. Cikin cikakken lokaci na zuwan Kiristi cikin jiki ya fara mulkinsa, da kuma za'a tattara kome a lokacin ikkilisiya, kuma wannan zai cigaba har sai dukan kome an tattara su kuma an sabunta su. Dukan abubuwan da za'a hada "dukan abu" sun hada da kome da yake cikin sama da kuma na duniya, ma'anar yawan mutane, al'adu, gwamnatoci, bangaskiya.

Wannan "duk abubuwan" ya bayyana a ko'ina a sabon alkawari, kuma wannan na nuna cigaban kawowa a karkashin kafar Kiristi na dukan makiyansa.Amma abun

mamakin anan shine yadda akayi wannan: ba ta karfin tashin hankali ba, ba ta finkarfi ba, ko kuma irin halin danniya, amma tawurin aikin sasanci na Ruhu cikin kamannin Kiristi na rayuwar mabiyansa.

Zamu iya cewa wannan sasanci ya kunshi abubuwa guda biyu: 1. Ga mutane na banbancin jinsi, al'adu, jinsi na maza ko mata, da kuma irin matsayin da muke da shi a ikkilisiya. 2. Tsakanin ikkilisiya da kuma duniya; yadda zamu kai mu kuma mu chanza makiyanmu. Ka tuna, wannan shine damuwar tsohon alkawari ce: menene zamuyi gameda makiyanmu, wadanda suke cigaba da tashi suna damun mu, duk da haka mun iya cin nasara da su? Kiristi ya nuna mana hanyar Allah.

*Na farko, sasanci cikin ikkilisiya:*

Wannan hanyar sasanci wata hanya ce wadda rayuwarmu ta sabunta kuma an kawo ta tare a wani iyalin mai lura na mulkin Kiristi. Mun zo da banbancinmu da kuma muna yin daidai da kamannin alamun kauna ta Kiristi, ba ga alamar wani mutum da al'adarsa ba. Allah Allah ne mai arziki da dama, wanda ake yin murna tawajen kauna, 'yanci da yin godiya.

Cikin babi na biyu na Afisawa munga wannan hanyar sasanci tsakanin masu bada gaskiya ga Yahudanci da Al'ummai. An kawo su cikin iyali daya, hadi da banbancin al'adu: saboda samun 'yancin bangaskiya kadai, wadannan al'adu an kawo su cikin mulkin Allah da kuma chanzasu su yi kama da kaunar Kiristi. Haka kuma, akwai babban 'yantawa, wanda ke ciki da tare a cikin duniyar Roma banda bishara. Wani babban abun mamaki ne. Wani abu ne wanda har ayau bamu kama ba, har a cikin masubi na banbancin yadda muka fito.

Bari mu dan juya wani gefe kadan. Ina tunanin wannan na da mahimmanci idan muka duba yadda muka tsaya amatsayin mu na ikkilisiya. Na yadda da wani bayani da wani lokaci naji: "idan da chanji ya tsaya can Afisawa sosai fiye da akan Romawa da kuma Galatiyawa, shekaru 500 da suka wuce sun zama daban." Wannan mutumin ba yana maganar matsalar dake da Roma ko Galatiyawa ba, amma hanyoyin da wadannan wasiku aka fahimcesu da aiki da su. Idan Afisawa sun zama abinda aka duba, kan maganar sasanci cikin Afisawa mai yiwuwa zai

kasance a bayyane gare mu, da kuma kasance a rarrabuwa da kuma aiyyukan Farisawa cikin harkokin mu wanda kowanne da kuma duniyar mu.

Wani abu da muka saba ji ne, “Idan wani mutum yayi wa’azin wata bishara, bari a zarge shi”, yayinda muka cikaga da kuma rarraba daga sauran masubi: kamar wannan wani irin halin tsarki ne. Ina bada shawarar daukar wannan ayar a cikin Galatiyawa tana daban da abinda Manzo Bulus yayi shiri. Manzo Bulus yana gyarawa  Bitrus akan wannan hanyar ta ruhaniyar Farisawa. Bitrus ya fito daga wadansu masubi saboda irin halayensu suna da ban. Ya dauki ‘yanci cikin bishara, kuma su sake gina katangar banbanci Kiristi ya raba da jininsa. Wannan yasa Manzo Bulus ransa ya baci.

Manufar manzo Bulus a Roma da Galatiyawa ba domin ya lalatar da irin hanyoyin Yahudawa bane, amma domin ya nuna cewa tunda ba shari’a ba daga bangaskiya, zamu karbar juna kome nene al’adarmu ko harkokin addinin mu zasu kasance. Bayanin Bulus kan shari’a ta bangaskiya shine domin ya janyo mu tare cikin jiki daya, domin mu kaunaci juna akan tebur daya na zumunta, koda yake wani yaci nama wani kuma bai ci ba. ba yana fada kan yin kaciya bane, amma akan matsin kaciya kamin yin zumunta. Bayanin Manzo Bulus acikin dukan wadannan litattafai na bishara shine na al’umma daban daban (kauna), ba domin rarrabuwa ba; ba wajen daukan matsayi ba da baya a sake rabuwa ba. Matsayin da muke dauka matsayin zumunta ne, ko da yake wadansu suna matsa mana domin mu rabu.

Wani abu mara kyau shine hanyar da muka dauki Manzo Bulus mara kyau shine a tarihin ikkilisiya yawanci muna yin tir da Yahudawa kuma muna tsananta musu saboda irin al’adunsu. Yi tunanin wannan, an kira ikkilisiya domin domin ta bauta da kuma ta sha wahala, ta zama mai tsanantawa wadansu. Wannan cikin bakinciki ya zama irin tsayuwar ikkilisiya har ya zuwa wannan zamanin namu na yau. Amadadin haka, ya kamata muna karbar al’adun Yahudawan  da kuma jawo su kurkusa domin sasanci  tawurin kaunar Kiristi. Wannan itace irin ra’ayin Manzo da kansa (Ayyukan Manzanni 15:20-21).

A shekaru 500 da suka wuce, irin wannan harkokin sun faru akan ikkilisiyar Roman Catolika da kuma irin al’adunsu daga Protestan. Akwai yawanci  kuskure da za’a gyara cikin rayuwar mu gaba daya, amma wadannan kurakurai za’a iya gyara su

tawurin amfani da ruhun sasanci. Wannan ce hanyar da zamu iya fahimta da sauraron juna yadda ya kamata, a maimakon rike tunani irin na girman kai "na sanin dukan kome" da dukan matsayi. Wannan ruhun na sasanci shine irin halin ikkilisiya. Zan bada shawarar cewa idan bama nuna wannan hali to bama rayuwa kamar wannan ikkilisiya kenan ba.

Yaya zamu ci jikin Ubangiji yayinda muna cikin rarrabuwa? Wannan shine abunda Manzo Bulus yake nufi da "ba tawurin rarraba jikin Ubangiji ba", da kuma yawanci mukan kasa gane jikinsa a sauran masubi. Iyalin Allah shine jikinsa. Manzo Bulus yana cewa, idan bamu gane jikinsa cikin sauran masubi ba, ko cikin masu talauci ba, to daga nan muna ci da sha ba daidai ba. Abincin Ubangiji ba na mutum daya bane, kayan mutum shi kadai ba, kamar yadda muke daukar shi ya zama, amma abincin yamma tare ne: sujada ruhu mai tsarki tare, al'umma, abinci tare, bada rayuwarmu ga dukan sauran jikinsa da kuma bautawa dukan al'ummar mu.

Wannan wani mahimmin bayani ne: daya, saboda rarrabuwar mu tana yaduwa akan gicciyen Kiristi, tawurin wanda ya rusa katangar da ta shiga tsakaninmu. Na biyu, yaya zamu dauki mataki na gaba, kuma mu zama masu sasanci, jawowa da sabunta karfi cikin duniya, yayinda bamu iya yin wannan ba a gidajen mu?

Zamu zama wadanda suka "aikata aiyyukan sasanci" da dukan wadanda suke kira sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi. Wadannan wasu aiyyuka ne da muke yi a sane ga masubi wadanda suke wajen zagayen zumuntar mu, fiye da chanji a ahalayenmu. Wani abun mamaki ne yayinda mutane suka kai ga yin sasanci da wasu sassan na ikkilisiya, yawanci akan dauke su a matsayin zindikai. Wannan shine abinda Yesu ya sha wahala, saboda ya ratsa layikan wasu. "Dan mutum bashi wurin da zai sa kansa." Ra'ayinsa shine yin nufin Ubansa, ba wurin zaman mu ba.

*Na biyu, bautar ikkilisiya da kuma sasanci cikin duniya:*

Afisawa tayi bayanin wannan hanyar.

"Anyi wannan ne kuwa domin a yanzu a sanar da hikimar Allah iri iri ga manyan mala'iku da masu iko a samaniya, ta hanyar ikkilisiya." Afiswa 3:10

Ikoki na nufin ikon ruhu dake iko ko yake mulkin rayuwar mutane. Wadannan na iya zama ikokin ruhaniya da suka tilasa, ko kuma ikon duniya, kamarsu gwamnati, bangaskiya, al'adu da kuma ikon arziki. Wadannan abubuwan sun hada su gaba daya kuma sun yi mulkin kasashe da duniya.

Ya kamata mu tuna kuma, cikin tsohon alkawarin, Allah yace zai dauki iko bisan dukan wadannan ikon da kuma, tawurin yin wannan, sake juyo da duniya. Yayinda muka zo wurin Yesu cikin bisharun nan, da kuma Manzo Bulus a cikin wasikun sa, munga yadda Allah yake kokarin yin haka. Hikimar Kiristi ba tawurin tursasawa bace, ko kuma yasa karfi irin na tunanin duniya, amma "wawancin Allah" shine yin bauta. Yanzu mun cigaba da wannan bautar tawurin ikkilisiya. Tawurin wannan wawancin na Allah ne,  "wanda yafi karfin hikimar mutane", wanda Allah ya shirya ya kawo ga ba kome ba wannan ikokin na duniya: wato, shawo kan  da kuma mu kauda ikokin su na shedan da kuma sasanta su cikin mulkin sa, domin ya albarkaci kasashen.

Mu tuna da matsayin mu. Yayinda yazo kan chanjin mulkin  ikkilisiya, mu ba pastocin gwamnati bane, wadda take manne ikonta kan rayuwar wadansu, daukar dama kan wadansu domin kungiyar da kuma manufar mu, yayinda muke yarda da rashin yin daidai na gwamnati. Muna shaidar gwamnati da rayuwarmu, kamar yadda Yesu ya nuna ga ikkilisiyarsa a gaban sarki Pilate. Yesu ba mai "nada sarki bane", amma annabi  ga sarakuna. Ikkilisiya tana bin Yesu. Sai mai shaida wanda ya kauda sonkai ya chanza dukan kanmu da kuma gwamnatin mu.

Mutane da yawa a kwanakin Yesu sunyi tunanin maiceto zaizo yayi dukan kome tawurin daukar iko. Wannan an ganshi a lokacin jarabawar Yesu, domin ya cika manufarsa ta Ishaya tawurin gwamnatin wannan duniya. A maimakon haka Yesu ya zabi gicciyensa, kuma ya kira mu muyi haka. Ya samu tasiri akan gwamnatin wannan duniyar wanda bazai sami kan ikkilisiya ba. wani abun ban mamaki ne na "sama da kasa" na hanyoyin Allah da aka gani cikin Kiristi. Babu wani abu a tarihi da ya shafi shugabanci fiye da gicciyen Kiristi, "wawancin Allah". Daukar gicciyen mu shine hanyar ikkilisiya. Yin bauta yana tabbatar da bayanin ikkilisiya da kuma haskaka haskenmu kan kasashen mu.

Shaidar mu tanakan Kalmar da aiyyukan Kiristi, fiye da ra’ayin sonkai, da kuma domin abubuwa nagari domin mutane duka. Shaidar mu itace domin sake gina al’umma a gida da kuma waje, domin salama cikin dukan kungiyoyi, domin nuna halin kaunar Kiristi wanda ya bada kansa domin dukan duniya, ba domin mu kadai kawai ba.

Bisaga ikon tattalin arziki da kuma al’adu, shaidan mu gare su itace nuna musu ikkilisiya mai kaunar al’umma, a maimakon neman kayan duniya da son kudi; kaunar juna a cikin ikkilisiya da kuma kaiwa cikin sauran jama’ar duniya masu shan wahala da irin wannan kaunar, maimakon nuna sonkai.

Gameda sauran bangaskiya, shaidar mu gare su shine bayani garesu da nuna irin wannan kaunar ga wannan al’ummar tawurin shaida bishara, “ba tunanin jin dadin kanmu ba, amma harda jindadi da bukatun sauran mutane”; bayan muna koya daga garesu irin alherin da muke samu, da kuma kasancewa shaidun Kiristi gare su tawurin Kalmar sa, alheri da kuma kauna. Wannan ba wani abun nuna abun adawa bane da kuma tsayuwar girman kai ba, amma wata tsayuwa da nuna alamar rayuwar Kiristi ga wadanda suke waje, kamar yadda aka gani cikin bisharar.

Koda yake shugabanni da yawa sunyi kokarin su sa kansu cikin addinin Yahudanci (Judaism) na karni na farko domin su kawadda bishara waje, da kuma ikkilisiya kuma sun sa kansu cikin kisan kai da yin Tsanani ga masubi da yawa, duk da haka masubi sun cigaba da haduwa cikin majami’u. Cikin yawancin majami’un makiya Kiristi ne, amma duk da haka masubi basu nuna kiyayya gare su ba. wannan tabbacin ya nuna cewa al’ummar masubi sun aikata cikin kauna ga sauran al’ummar Yahudawa da kuma cigaba da sujada tare da su.

Tun daga wannan lokacin babban rashin girmamawa ya daukaka kuma ya lalata dangantakarmu da al’ummar Yahudawa. Irin wannan yanayin ya shafi zumuntar mu da al’ummar Islam da kuma sauran al’ummai na bangaskiya. Bishara da irin bukatar darajar ta na bukatar muyi shaida kowanne lokaci da kuma fayyacewa amma da girmamawa, ta yadda muka shiga cikin rayuwar wadansu, da kuma girmama al’adunmu, wurin yin bauta da bada kai da kuma yin gafara yayinda aka yi mana wani ha’inci.

Muna ainihin burin alkawarin Allah ya cigaba, domin kogin ruwa ya zubo daga ikkilisiyarsa, wanda ke kawo Kalmar rayuwa daga jagorancin ruhu mai tsarki da kuma iko ga dukan al'ummai da kuma mutane, da kuma chanza kasashen tawurin irin 'ya'yan da muke bayarwa.

A takaice, ikon Allah da yake kawo mana ya hada da wadanda suke cikin halayenmu, da kuma irin yanayin mu. A nan ne inda ikon yake zaune kuma yake yin aiki daga wurin. Manzo Bulus ya lissafa irin wadannan iko cikin littafin Korantiyawa: halin rarrabuwa na ruhu, rashin hadin kai, fasikanci, sonkai na daukar wadansu zuwa kotu maimakon shanwuya ba daidai ba, watsar da talakawa, nuna daukakar ruhaniya, babu daukar al'adu da kuma ra'ayin sauran mutane: duk abinda ya kaucewa mulkin kauna.

Dukan wadannan nuna sonkai ne, suna hallakar da ikon al'umma. Yayinda aka hallaka al'umma, daga mutane sukan sha wahala. Allah, tawurin sabon mulkinsa cikin zukatanmu, baya kaunar wannan shan wahalar. Allah ba ya kauda wannan da karfi ba, amma tawurin sabuntar zuciyar mu. Idan Allah ya kawar da fin karfi ba da jinkai ba muma zamu hallaka. Wadannan sune ikon da Allah yake kawo wa kasa cikin  ikkilisiyarsa, yayinda yake sabunta rayuwarmu a cikin junanmu, da kuma yake aika ikkilisiyar a matsayin  sabon jiki da za'ayi shaida cikin duniya. Allah yana sake gina mu cikin sabbin ikonsa na 'ya'yan ruhaniya.

Wannan shine manufar Allah cikin Kiristi, wanda yake kan wannan  jikin: domin ya sasanta da kuma sabunta dukan  halittarsa. Dukan bisharar za'a iya sasanta ta cikin manufarta, a cikin makomarta, cikin ruhunta, da kuma cikin irin shirinta. Allah ya fi karfin makiyansa tawurin sasanci, da kuma yayi amfani da bada rayuwar mutanensa domin  yin haka, kamar yadda ya nuna mana cikin Kiristi, wanda ya bada kansa domin dukan mu. Idan akwai wata Kalmar da za'a iya kwatanta bishara shine sasancinta: wanda shine domin gina kasashen mu tawurin duniyar Kiristi chanjin al'ummar mu, cika alkawarin da Allah yayiwa Ibrahim.

"Don ta gare shine aka halicci dukkan kome, abubuwan dake sama da abubuwan dake kasa, masu ganuwa da marasa ganuwa, ko kursiyai, ko masu mulki, ko masarauta, ko masu iko, wato dukkan abubuwa an halicce su ne ta wurinsa, shine kuma makoma tasu. Shine gaba da dukan abubuwa, dukkan abubuwa kuma shi ne

ke rike da su. Shi ne kai ga jikin nan, wato ikkilisiya. Shine tushe, na farko masu tashi daga matattu, domin ta kowanne abu ya zama shi ne mafifici. A gare shi dukkan cikar Allah na farin ciki da haka, da nufin tawurinsa Allah ya sulhunta dukkan abubuwa da shi kansa na kasa ko na sama, yana kulla zumunci ta jininsa na gicciye." Kolosiyawa 1:16-20

"Cikar Allah zata cika dukan kome", har sai "sanin daukakar Ubangiji ta cika dukan duniya, kamar yadda ruwaye suka cika dukan rafuka."

Maganar Allah ba labari kawai bace; ga Yahudawa tabbacin alkawarin Allah ne. lokacin da Isra'ila suka fito daga Masar suka ga labarin tarihin halitta an maimaita shi a rayuwarsu. Allah ya kawo sabon wata kasa dake cikin tashin hankali, ya basu kasa mai kyau kuma ya maida su 'ya'yan sarakunansa, domin su nuna alamarsa ga kasashe dake bauta. Sune sabbin Adamu na Allah cikin duniya. Wannan manufar ceton, domin sa albarka ga kasashe, dukan kasar duniya, Allah ya watsar da ita lokacin da Adamu da Isra'ila suka fadi, amma an cika shi tawurin Kiristi a cikin ikkilisiyarsa. "Amma ku zababbun mutane ne, 'ya'yan sarauta na ainihi, tsarkakakken birni, Jama'ar Allah na musamman, domin ku iya bayyana yabonsa wanda ya kira ku daga cikin duhu zuwa cikin muhimmin haskensa." Wannan shine bayanin tarihin labarin halitta a cikin ikkilisiyar bautar.

Wannan hujjar ta zama dalilin matsayin ga tauhidin yamma wanda manufarsa wani lokacin ta kauce daga irin ganinmu: wato alamar Allah da aka gani a cikin Kiristi ya kamata a ga wannan tawurin iyalinsa na cikin nan duniya domin 'yantar da halittarsa daga daurewarta. Dukan duniya ta zama kasar alkawari na mai kyau ta Allah.

**Yaya Ainihi Kamar Allah Take?**

Ra'ayinmu na Yesu yana cikin bayanan bisharu maiyiwuwa ya zama wani kalubale daga wani sashi na maganar Allah. Mun sani cewa a wurin Kiristi mun gani a fili ainihin yanayin Allah. Wato nufin Allah, ya aiko Kiristi domin mu iya hakika saninsa kuma mu zama kamar shi. Wannan itace kadai hanyar da zumuntarmu da kuma duniya zata warke.

Amma a wani sashin na maganar Allah, kamar yadda yake a wani sashin na tauhidin mu, Allah zai iya yi kamar mai tashin hankali.

Yayinda hankalin mu ko wa Allah yake, da kuma kamar yadda yake, yana shafar rayuwarmu a matsayin mu masubi. Irin kamarnin mu na Allah yana da mahimmanci, saboda an chanza mu zuwa cikin alamar da muke yiwa sujada da kuma muke nunawa cikin duniya. Wannan shi yasa alamar Allah cikin Yesu Kiristi take da mahimmanci kwarai. Idan muka dauki wadansu alamu, ko kuma hoton da ba daidai ba na Allah, zamu iya zama da damuwa a cikin rayuwarmu da kuma masu tashin hankali a al'ummanmu.

Wannan ya sha faruwa a cikin tarihi sau da dama. Yawanci ikkilisiya tana iya sa matsayi mara aminci akan makiyanta. Mun tabbatar da ita daga cikin nassoshin maganar Allah da muka dauka ba daidai ba da kuma tauhidin da bai nuna yanayin Allah ba kamar yadda yake cikin Kiristi ba.

Mun hadu da zabe kala-kala a yau akan irin yanayin da muka nuna, kuma dole mu nuna ainihin ra'ayi na daidai na littafi maitsarki a matsayin almajiran Yesu. Wannan yana da mahimmanci gare mu, bari mu duba dan ra'ayi kadan da zai nuna hoton irin yanayin Allah.

1. *Mulkin Allah yana zuwa tawurin Yaki da kuma hallakarwa.*

Za'a iya daukar wannan daga cikin nassoshi kamar su Matiyu 24, inda Yesu ya fadi "yaki da kuma muryar yaki", ko kuma daga cikin Bitrus ta 2, inda Bitrus yayi maganar duniya zata kawo hallakar wuta. Zamuga wannan cikin littafi na da ake kira Sakedubawa na Ruya, don haka b azan sake maimaita wannan bayanan acan ba.A cikin al'adun yamma yawanci mukan fassara wannan nassoshin daban, muna

amfani da wannan nassoshi na ka’idodin yaren Girka da al’adunsu, ba na Ibraniyawa ba.

Babban bayanin da za’ayi anan shine wannan shine yawan Yahudawan da akayi tunanin mulki zaizo a cikin karni na farko.sunyi tunanin zaizo tawurin Allah ya hallakar da makiyansu. Yesu ya fili yaki yarda da wannan ra’ayin.

Ina cikin ikkilisiya wani lokaci (kuma wannan ya faru a lokatai da yawa ) daga nan sai wani dan’uwa yace dani, “Allah yana amfani da Amurka ya hallaka kasashen Arab akwanaki na karshe…..”, sai ya cigaba. An gaya mani cewa zakaje ta masallaci domin kaji wannan bayanan na tashin hankali! Hakanan ma zakaji shi a ikkilisiyu kamar haka.

2. *Allah mai hukunci mai zafi ne*

Ra’ayin anan shine, tunda Allah shi Allah ne mai hukunci, to hukuncin mu za’a ‘yantar da shi. Sau nawa mukaji gameda ‘yancinmu mu sami “bacin zuciya na gaskiya”, kamar muna iya yin wadannan abubuwan? Bamu chanchanci wannan ba,wanda shi yasa maganar Allah tace, “daukar martini nawa ne, inji Ubangiji.”

Amma hukuncin Allah bai nuna shi ya zama mai tashin hankali ba. wani mahimmin wuri wanda maganar Allah tace an kwatanta hukunci Allah cikin Romawa 1. A nan kalmomin da akayi amfani da su da maimaici sune “mikawa a hannu”, “bayarwa gaba”. Hukuncin Allah ya hada da mu kauce kiyaye kariyar dake kewaye da mutum, daku barin shi ya cigaba da hanyarsa. Hukunci wani daukar hanyar chanza irinr ra’ayi. Mune mukeyin haka, yayinda muka ki yin gyara. Yayinda wannan ya faru, mutum yana kawowa kansa sakamakon irin aiyyukansa da yayi. Allah baya yin tashin hankali kan mutum ba.

3. *Allah ya aiko da wuta kan Sadoma*

Littafin Ayuba ya bamu bayani kan wannan. A nan, shedan ya bayyana a gaban Allah, yana kalubalantarshi kan bayanin Ayuba. Allah daga nan ya cire kewayen da ke kan Ayuba ya bari a gwada shi. Shaidan ya fita daga gaban Ubangiji daga nan ya aika da cututtuka kan Ayuba tawurin yaki, yanayi da kuma wuta. An fadi cewa, “Wuta daga wurin Allah daga cikin sama ta sauko kasa”, Yayinda wutar take ba

daga wurin Allah ba. Wannan itace hanyar da Ibraniyawa suka bayyana masifa cikin tsohon alkawari, domin irin bangaskiyarsu ta sosai akan Allah mai girma.

Munga irin bayani da aka bayyana gameda Sadoma da kuma ruwan Tufana. Hukuncin Allah ya hada da kauda kewayen da ke kewaye da mutanensa domin su karbi sakamakon hukuncin aiyyukan da suka yi. Sakamakon faduwar mutum ta shafi inda muke rayuwa da kewayen mu. Sashin Allah shine kasancewa da hakuri, da kuma nuna jinkai da kuma, bayan hukunci, ya sake ginawa da kuma sabunta kasar.  Amma Allah bashi da sashi cikin tashin hankali wanda ke kawo hallaka ga rayuwar mutum.

4. *Allah ya kashe 'ya'yan fari na Masarawa.*

Hakika bai yi haka ba: "Mala'ikan Ubangiji ne" da kuma wannan yayi kama da Kalmar dake cikin Ayuba. Wadannan Mala'iku ne cikin mulkin shedan, dake cikin cikakken yaki da Allah. "Mala'ikan Ubangiji" na iya nufin ko dan aike mai kyau ko mara kyau. A cikin littafin Ayuba ana kiransu "'ya'yan Allah". Dukan halitta ta samo asali daga Allah kuma ya baiwa halittarsa dama na yin zaben ko zasu bautawa abu mai kyau ko mara kyau, harma ga mala'iku.

Allah ya gwada Ibrahim. Ya jaraba Dauda ya kidaya Isra'ilawa da kuma maganar Allah tace ainihin Shedan ne yayi wannan, bisaga faduwar Dauda cikin shari'a. "Ruhu mai karya daga Allah" sun kautar da sarki zuwa hanya mara kyau. Dukan wannan yana nunawa ga ikokin ruhaniya a yaki da halittar Allah. Wannan ya nuna tabbacin gaskiyar yanayin Allah: ya sha wahala da kwamiti da kuma makiyan shedan domin su gwada shi.

A masar, Allah "ya sa gaba" Isra'ilawa domin kare su ga mai hallakarwa (duba Ishaya 31). Kalmar nan sa gaba na nufin Allah ya tsaya tsakanin mutanensa da mai hallakarwa. Allah ba shine mai hallakawar ba, amma mai yin ceto.

5. *Hukuncin Allah daga cikin daji*

"Doka tana kawo hukunci".  Mai hallakarwa a cikin jeji ba Allah bane, amma mai hallakarwa (1 Korantiyawa 10:10). Shedan ya tsaya domin ya tuhumi Allah domin kawo mutane marasa tsarki daga Masar. Munga iri daya lokacin da Allah ya fito

dasu daga Babilon (Zakariya 3). A cikin jeji Allah yace zai hallakar, amma wannan na nufin zai bada dama ga maihallakarwa. Hakika, mai tuhumar Allah yayi jagoranci zuwa zunubi da kuma ta haka "ya sace, yahallakar ya kashe".

Banbanci tsakanin Allah mai kauna wanda ya 'yantar da mutanen sa daga zaman bayi da kuma Allah na wuta akan dutsen. Ya kira su zuwaga zumunta, su zama mutanensa kuma su nuna kaunarsa cikin kasashe. Amma kamar Adamu, suma suka ki su bada gaskiya ga kaunar Allah kuma suka karbi abokantakarsa. Domin haka suka koma wajen shedan a cikin zukatansu kuma suka zo karkashin mulkinsa da kuma suka bukaci doka ta cece su. Doka tana bukatar son kasa, yaki da mutuwa su kasance, amma wani yanayi ne Isra'ila suka zaba saboda rashin bangaskiya. Allah yace za'a kamasu tawurin doka cikin tarkon shedan (Maimaitawar Shari'a 28, Romawa 7). Doka, kishin kasa da yaki suka kasa su kauda zunubi, har a Isra'ila ita kanta.

Yayinda kake shakka gameda ma'anar wannan nassin na maganar Allah akan yanayin yadda Allah yake, rashin cika umurni ga Yesu Kiristi cikin bisharunnan, wadanda suka ki su kira wuta kasa kan masu zunubi, amma suka ce "Uba ka gafarta musu". Kada ka koma wajen Farisawa domin ka tuhuma da kuma hallakarwa.

6. *Tsarkakewar Kabila a cikin Joshuwa*

Wannan ra'ayin ba gaskiyar bayanin Joshuwa bane. Joshuwa ya kai farmaki ga kungiyar sojoji. Kalmomi kamar, "Yasa ga takobi dukan abinda yake numfashi, namiji, mace da kuma yara", ba hakanan suke ba, amma bayanin Magana ne. nassi cikin Joshuwa shi kansa, hadi da wadansu tsaffin takardun, sun nuna wannan. Akwai litattafai masu kyau da suke nan wadanda suka kalli wannan cikin bayani sosai, a misali shin Allah shi dodo ne mai akida? Daga Paul Copan.

Sabanin nufin Allah na hukuncinsa, abinda muka gani cikin Joshuwa shine Allah wanda yace, "Lokacin da ka shiga cikin kasar, ka kaunaci bakin kasar, kamar yadda na kaunace ka kuma na kawadda kai daga bautar zunubi". Manufar Mulkin Kiristi shine domin a chanza al'adunmu zuwa ga yanayinsa na kauna.

Allah ya bayyanawa Isra'ilawa cewa kada suyi wani sarki, kada su zama kamar kasashe kewaye dasu, kada su gina daular soja, ko kuma su tattara dukiya ko dokoki, da kuma kada su rike sojojin tsaye, amma su kaunaci makwabtansu, su yi aminci ga mutanensu kuma su kaunaci makiyansu, da kuma Allah zai lura dasu. Wa'azin kan tsauni ba sabo bane. Daular da Sarki Dauda da Salomon suka gina ba nufin Allah bane. Koda yake suka basu alherinsa da dukiyarsa, duk da haka basu samu kaya kamar na fili ba.

Cikin Joshuwa mun ga "runbu" akan dukan bautar gumaka, amma cikin Yesu bamu ga wannan ba. Yesu bai jawo masu zunubi daga kasar ba. Ya bada rayuwarsa ga makiyansa, domin su chanza ra'ayinsu. Wannan ya tada hankalin Farisawa da kuma Yesu ya kira su domin su nuna jinkai ga mutanen Allah.Runbun Joshuwa ba shine irin yanayin Allah ba, amma Yesu ne.

7. *Kaffara*

Nazarrin kaffara ya zama wani abun da ya zama ko'ina acikin wannan zamanin namu amma yafi nuna yanayin mutane da aladunsu fiye da yadda tayi ga Allah. Wannan nazarin ya bayyana cewa Allah kamar sarkin mutane ne wanda za'a iya bata masa rai tawurin yin ba daidai ba gare shi, da kuma Allah, kamar wannan sarkin, dole ya sami a biya shi, diyya da biyan sakamako.

Wannan ba shine ra'ayin ikkilisiya ta farko ba. Har ya zuwa yau, ba irin ra'ayin da dukan  masubi suke rikewa bane. Kuma bisharu sun nuna irin ra'ayi daban akan kaffara, inda Allah yake gafara a sauwake, da kuma yake neman masu tuba kawai. Yesu ya gaya mana cewa muyi gafara cikin sauki, ba tare da wani sakamako ba, gama wannan ne abunda Ubanmu yayi. Yesu bai yarda da sakamako ba (wato "ido domin ido"). A labarin yaron nan almubazzari, Ubansa ya gafarta masa da kuma dukan sauran 'ya'yansa suka komo, ba tare da wani sakamako ba. A wasu lokutta, Yesu ya fadi cewa, "zunubinka an gafarta maka……"

Cikin bisharu, aikin Yesu and ganshi kamar aikin ceto daga Shedan, daga zunubi, daga mutuwa da kuma daga dokoki. Yace, "me zai hana wannan matar, wadda ke duk wannan shekarun daya na shedan a sake ta a ranar Asabar? Ranar Asabar da ranar bukukuwa anyi sakin daurarru shedan, kamar fitowa, saki daga sarkin

Fir'auna. Yesu daga nan ya kwatanta irin mutuwarsa ta kaffara a matsayin "hanyar ceto ga mutane da yawa."

"Gama dan yazo ba domin a bauta masa ba, amma domin ya bauta, da kuma ya bada rayuwarsa a matsayin ceto ga mutane da yawa", wannan ya zama wata alama na yanayin yadda Allah yake da kuma tsayuwarmu a matsayin ikkilisiyarsa da kuma masubin sa.

Ikkilisiya ta farko ta ga gicciye a matsayin Allah "yana shiga gaba" namu: wato, tsakaninmu da shedan, wanda yake daidai a shari'ance na sa Allah ya cigaba da tsare matsayi cikin dokarsa, amma ba daidai ba a irin ra'ayinsa. Allah ya tanada kuma ya cika duk wani yanayi na

(ya haifi hukunci domin rashin biyayyarmu) domin ya cece mu a hanyar mai sauki, ya bayyana kaunar shi da kuma tsarkake tunanin zukatanmu. Ya dauki hallakar mai tuhumar da kansa. Bai yi wani tashin hankali ba da kuma neman wani tashin hankali ba. Dukan wani tashin hankali wanda mutum yayi ne, wanda Allah ya dauke da kansa cikin Kiristi domin ya cece mu daga zunubi, mutuwa da dokoki. Kiristi ya tashi domin ya bamu rain a har abada. Kamar yadda wani aboki yace, "Yesu bai cece mu daga Allah ba, amma ya bayyana mana Allah a matsayin maiceto".

Ko a lokacin hadaya dabbobi a cikin tsohon alkawari ba nufin Allah bane. Ba mutane da yawa ba tsohon alkawari zasu iya duba baya su ga irin yakin da akayi tsakanin Allah da zunubi, su ga ainihin irin bada kan yanayin Allah. Amma wadansu annabawa sunyi kuma sun bayyana irin halinsu na hakika, kamar yadda Yesu ya nuna shi.

Gicciye gaba daya ya tabbatar da dukan nunin Allah duka na kin tashin hankali, nunin dan yatsa da karkatacciyar kuka mai dadin hawa wanda yake gado cikin zukatan mutane da al'adunsu. Ya haifi dukan wadannan, amma ba wanda ya nema.

Muna kwaikwayar gicciye, ba tawurin ne man sakamako ba, amma tawurin yin gafara cikin sulhu da kuma mika kan mu a matsayin bayi ga 'yan'uwanmu maza da mata, ga al'ummarmu da kuma ga makiyanmu. Mun kwaikwayi gicciye tawurin

sabuntawa, (kauna, gafara) adalci, ba tawurin nuna son hukunci ba da kuma son jin dadi ba wadanda sukayi rayuwa kamar Allah cikin Kiristi sune 'ya'yan Allah.

Yayinda muke cikin shakka gameda tauhidin mu, mu dubi Yesu da abinda ya koyar da kuma abinda yayi ko zamu koma tsohon alkawari, ko kuma cigaba zuwa Manzo Bulus da kuma Ruya ta Yohana, mu fahimta abinda akace cikin Yesu.

8. *Hukunci na har abada.*

Wuri bazai ishe mu duba wannan sosai ba. zamu iya tabbatawa da Ibrahim, "Shin ba mai hukunci dukan duniya zai yi abinda yake daidai ba?" Wannan na nufin a gaban masu tuhumarsa, agaban zuciyar mutum, da kuma a hasken dukan alherinda ya baiwa dukan duniya. Allah bai yi kamar mugun shugaba ba, ko dayake yana da 'yancin yin haka.

Masubi suna da ra'ayoyi dabam –dabam akan yanayin hukunci na har abada, ko a karshe za'a hallakar da rayuwar masu zunubi, ko kuma hallakar da rayuka harabada cikin jahannama. Ya kamata mu tafi tawurin maganar Allah, bisaga yanayin ta, ba tawurin namu ra'ayin da kuma irin tunaninn mu da na kungiyoyinmu ba. Akwai  nassoshi da yawa cikin tsohon alkawari da kuma sabon alkawari. Yawancin wasu nassoshin sunyi amfani da alamu, domin daukar matsayi akan dukan bayanai wasu zasu iya iza mu muyi daidai.

Wannan darasi ne mai ma'ana, amma zamuyi kuskure idan mukayi amfani da irin koyarwar azabar zuciya ta harabada, wanda ta zama sananniya a wannan zamanin namu, domin nuna yanayin yadda Allah yake, kuma muyi amfani da wannan domin mu tabbatar mun nuna hali irin na rashin kauna zuwaga wadansu.

Tawurin yin biyayya ga Kiristi, ainihin darasi da zamu dauka daga wannan nassoshin kan hukunci shine cewa Allah mai hukunci ne kuma wannan ya koya mana kada muyi hukunci, yin tsegumi da yin gulma akan wadansu, amma a maimakon mu bada kanmu garesu cikin kalmomi da aiyyuka. Lokacin da aka warkar da Na'aman daga kuturta, ya tambaya cewa Ubangiji bai dauke shi bakin kome ba shi kuma ya fadi yana yiwa sarkin sa sujada a wurin sujada. Ya fadi a cikin zuciyarsa zai yiwa Ubangiji sujada. Allah yana ganin zukatanmu, duk inda muka

duka muka yi sujada. Yesu ya fadi wannan abun sau da yawa ga Yahudawa zamaninsa. Kada kayi shari'a, amma ka taimaki wadansu.

Allah bai taba tambayar mu muyi abunda shi bai taba yi ba. yana rokonmu muyi gafara cikin sulhu saboda shima yana yin gafara cikin sulhu. Yana sa mu kaunaci wadanda basu da masu kaunarsu saboda shi da kansa yana kaunar wadanda basu da masu kaunarsu. Yasa muyi abunda yake daidai a idanuwan dukan mutane, saboda shi da kansa bayayin abunda bashi da kyau ga mutanen da ya halitta. Idan muna tunanin Allah yayi hali mara kyau, to daga nan muma zamuyi haka ga wadanda muke tunanin suna karkashin mu.

Irin ra'ayinmu na Allah yana shafar yadda muke bida mutane cikin aurenmu da kuma irin rayuwar da muke yi. Ta hanyoyi da yawa wadannan ra'ayoyi suna bukatar chanji. Yawanci mun gan shi a matsayin ubangiji mara adalci kuma mun sa shi cikin irin zumuntarmu da sauran mutane. Allah yana aikata kaunarsa ga halittarsa. Mu zamu 'ya'yan Allah: muyi kamarshi. Wato abunda ya tambaya.

9. *Gwamnati na da takobin yin kisa*

Manzo Bulus ya fadi wannan gameda gwamnatin kasar Roma 13. Ya kirasu "Ma'aikatan Allah" wato a ma'ana yana kyale muguwar gwamnati domin su kauda mugayen mutane. Dole a girmama su, kamar yadda Daniyel ya girmama sarki Nebukanazer. Wannan ba yana nufin wannan gwamnatin tanayin nufin Allah ba. manzo Bulus yana Magana kan maibi ya girmama da kuma daukaka gwamnatin dake mulki. Bulus bawai bai sani ba ga rashin adalcin gwamnatin Roma ba, kuma ya shaida ga Ubangiji Kiristi akan wannan. Ruya ta Yohana ta kwatanta wannan gwamnatin a matsayin dabba.

Maganar Allah ta nuna cewa a chanza gwamnatoci kuma a sabunta su, domin suyi hukunci cikin adalci da jinkai, ba tawurin daukaka kansu bisan mutane ba, amma su zama da kaskanci kuma su bautawa mutane cikin mutunci da jin dadi, kamar yadda Allah yake yi. Gwamnatoci basu da lasi daga wurin Allah suyi bautar kasa da ra'ayin kansu ba, bayan basa lura da mutane, maiyiwuwa ma taimakawa wajen shan wuyar sauran mutane.

Muna bukatar muyi lura yadda muke amfani da maganar Allah wajen samo "maganin matsalar sojoji." A kowanne wuri inda masu tashin hankali suka sami asali dole akwai rashin adalci na wani dogon lokaci wanda ya gyara musu wurin domin wannan. Cikakken al'umma mai hadin kai ta samo asalin siyasarta maiyiwuwa daga irin yanayin martanin da suke da shi fiye da irin rashin adalcin da zasuyi. Al'umma irin ta rayuwar ikkilisiya tana bukatar shaida domin lura na wannan sashin, duk da irin yawan wannan mutanen addinin ko kuma 'yansiyar. Wannan yana warkarwa. "Sakamakon adalci shine zai kasance salama."

Gwamnatoci musamman suna gina dauloli. Allah yana son mutanen sa su zama misali ga wadansu kuma su gina al'umma da zata sabunta ikon duniya. Saboda haka, ga masubi Manzo Bulus yace, ku sami chanji kamar yadda kamannin Kiristi suka chanza:

"Kada ku koma kamar irin yanayin wannan duniyar, amma ku chanza tawurin sabuntawar zuciyarku. Ta haka zaku iya gwadawa da chanza abunda ke nufin Allah – mai kyau, mai jin dadai da kuma cikakkiyar manufa…… Dole kauna ta zama tabbatacciya. Kuki abunda ke na mugunta; ku rike abunda ke nagari. Ku mika kai ga juna cikin kauna. Ku girmama juna fiye da kanku. Kada ku rasa yin kokari, amma ku ajiye jinkanku na ruhaniya, kuma bautawa Ubangiji.ku zama da farinciki cikin bege, hakuri cikin damuwa, bangaskiya cikin addu'a. ku shaida da mutanen Allah wadanda suke cikin bukata. Ku kwatanta liyafa. Ku albarkaci wadanda suke tsananta muku; kusa albarka kada ku la'anta. Kuyi farinciki da wadanda suke farinciki; kuyi bakinciki da masu bakin ciki. Ku zauna cikin kwanciyar hankali da juna. Kada ku girmama kanku, amma ku iya yin zumunta da mutane wadanda suke kasanku. Kada ku zama masu fadi rai. Kada ku rama mugunta da mugunta ga kowanne mutum. Kuyi hankali wurin yin abinda ke daidai a idanuwan kowanne mutum. Idan zai yiwu, bisaga yadda ya dogara gare ku, ku zama da salama da dukan mutane. Kada ku nemi daukar ramako, ya 'yanuwa na, amma ku barwa Allah domin hukunsa, gama an rubuta: "Nawa ne daukar fansa; zan nemi sakamako," inji Ubangiji. a tawani sashin kuma: idan makiyinka yana jin yunwa, ka cida shi; idan yanajin kishi, ka bashi wani abu domin ya sha. Tawurin yin wannan, zaka doka garwashin wuta a bisan sa (zaku taba zuciyarsa). Kada kabar mugunta tafi karfinka, amma kafi karfin mugunta da abu mai kyau."

A dukan wadannan sassa, Allah wanda yake kauna, wanda yake mai tsarki da adalci, yana aiki cikin duniya mai zunubi da makiyinsa Shedan, yana aikin cikin sabon mulkinsa domin ya chanza zukatanmu da kuma kasashen mu akan irin kamanninsa, ya bayyana mana cikin cikarsa ba tare da illa ba cikin Yesu Kiristi. Tafiya cikin maganar Allah tare da mahimman kalmomi, mun gani cewa Allah bayason tashin hankali.

Munga yanayin Allah a yanayin abunda yakeyi gameda makiyansa. Yana bauta musu, da kuma tayin haka yana bayyana manufarsa gare mu domin mubi. Yana chanza mu zuwa ga kamanninsa, har sai, “munsa kayan yakinmu cikin kayan salama”, da kuma “har sai karen jeji ya kwanta da dabba.” Wannan shine yanayi da kuma shirin ikkilisiyar shi.

**Menene Almajiranci?**

Ka duba irin yanayin da duniya take a yau! Yaya ta kasance haka? Addini yana cikin wannan. Shin wannan ne Allah ya bamu sani a kansa, domin mu rarraba bisan abubuwa? Mun koyar da sanin Allah, kamar wannan shine mutane suke bukata, amma ba almajiranci ba tawurin bishe su da misali ta hanyar Allah ba. Bamu yi abubuwan da Allah yayi ba, saboda bamu san shi ba, bamu san ainihin irin yanayinsa da kuma yadda kamarsa take ba. Duniya tana bukatar warkarsa da kuma domin haka muna bukatar babban chanji. Cikin dukan kome, Yesu ya koyar cewa samun warkarwa zai farad a mutane Allah, zamu cire gungumen dake cikin idanunmu. Chanji zai fara a cikin gidajenmu na bangaskiya. Domin haka ga wadansu sassa nan da muka sa domin dubawa:

1. *Abunda mukayi ne, ba abinda muka bada gaskiya ba.*

Mun riji'a kan bangaskiyarmu, kuma wannan ya rarraba mu daga 'yan'uwanmu a cikin ikkilisiya da kuma sauranmu a wajen ikkilisiya. Wannan rarrabuwar shine babban abunda ya zama damuwa kwarai gare mu a yau da kuma dalilin da yasa duniya take cikin babban yanayin da take ciki. Muna gina babban sansani da kuma bama iya yin kauna da kuma taimakon makwabtanmu. Addini yana cikin abubuwan da suka rarraba mu, amma duk a cikin koyarwar Yesu wannan ne ya kamata ya jawo mu zuwaga makwabtanmu, domin mu taimakesu da kuma lura da su domin bukatarsu, ko ma wanne irin makwabci ne yake. Menene ya zama da damuwa da zukatanmu? Me yasa muka juya koyarwar Yesu da kuma irin rayuwarsa ta koyo sama da kasa?

A cikin koyarwar wa'azin kan dutse, Yesu bai koyar kan abunda muka bada gaskiya ba, amma yayi Magana kan abunda mukeyi. Yayinda muka duba kowanne sashi na wannan wa'azin yana Magana kan irin rayuwa da mukeyi.

Babu inda cikin wannan wa'azi dake da tsarin abubuwan da ya kamata mu bada gaskiya kansu.ka yi tunanin wannan. Wa'azin kan dutse ainihin jawabin Yesu ne na yadda za'a iya zama almajiransa. Mun yi tunanin cewa

almajirantarwa shine sa mutane cikin ajin koyarwa akan tauhidin bangaskiyar mu; ba mamaki muke a matsayin da muke yau.

Almajirantarwa shine yadda zamu bi Yesu cikin zumuntar mu da sauran mutane, domin muyi sasanci, mu bada rayuwar mu wajen taimakon warkar da al'ummar mu. Almajirantarwa shine mika kan mu cikin bangaskiyar mu, tawurin ruhunsa dake zaune cikin mu, mu kaunaci juna da kuma mu kaunaci makiyanmu: mu lura da bukatunsu na jiki. Kauna tafi gaban dukan bukatun mu na dukan rayuwa, kamar yadda yake a rayuwar Yesu. Wannan shine abinda ya koya mana kuma ya kira mu bishi a matsayin almajiransa.

A kwanakin Kontastine, shugaban Roma kirista na farko, dadi da kuma yanayin ikkilisiya cikin duniya ya chanza. Kontastine yasa hadin kai cikin mulkinsa dole kuma ya sa bishop suka "yarda" akan tauhidi. Suka shirya Nicene da kuma shirya anathema: "la'ananne ne kowanne mutum da bai bada gaskiya ba" wannan shine sharing mahimman abubuwa. Sun sa horo ga "bidi'a" kuma suka sa marasa bi ga takobi. Augustin masanin tauhidi, hakika ya tabbatar da abinda ya kira "tsanantawa" masu yin bidi'a tawurin hadin karfin gwamnati da ikon ikkilisiya. Wannan gaba daya ya juya matsayin Yesu ("mulkina baya amfani da iyawar wannan duniya") akan matsayin ta.ikkilisiyu sun tsaya kan matakin ra'ayin Augustin, ga babban matsayi, har ya zuwa yau.

A lokacin Kontastine ne cewa yadda ya kamata a zama almajiri ya chanza. A maimakon mika rayuwar mu domin sauran mutane, muka zama warware zuwa kungiyoyin siyasa bisaga tauhidin mu. Sai wani Yesu kuma wanda ba'a gane bay a zama shugaban mulkin mu na wannan duniya.

Yakubu yayi bayani kan wannan matsala. Ya rubuta kamin Urshalima ta fadi a karni na 70 AD, lokacin da wannan yankin yake cikin babban damuwa, kusan alamar yadda abubuwa suke a duniya yau. Rarrabuwa da kuma rashin lura da sauran mutane ya cika. Yakubu yayi bayani kan abubuwan warkarwa. Yayi bayani kan ainihin bangaskiya, ko kuma tabbataccen almajiranci, da cigaba.

Zamu iya daukar tsari da sauri daga Yakubu: girmama dukan mutane da daukaka daya, komene matsayinsu ko kuma daga inda suka fito; kada mu shari'anta da kuma yin Magana mara kyau kan wadansu; ku tuba daga kowanne irin halin tashin hankali (son kai da kuma fasikanci); mu lura da matalauta; mu lura da dukan wadanda suke cikin bacin rai; mu sa su bisan abinda muka mallaka; kada mu nuna bangaskiyar mu da akidarmu, amma irin ayyukan mu ga sauran mutane.

Yaya zamu iya tuka mutum mai jin yunwa da sauri cikin mota kuma muce mun bada gaskiya kan abubuwa na daidai? Yaya zamuyi banza da masu shan wahalar gudun hijira, mutanen jirgin ruwa, musulmi, marayu, gwauraye, yara matalauta, da kuma sauran al'adu cikin al'ummar mu, marasa arziki (yawanci mata), ko kuma 'masu zunubi' domin kawai basa cikin mu? Yayinda muka bauta musu mun sami warkarwa. Yayinda muka nemi wadansu mun sami kanmu. Mun sami warkarwa tare. A lokacin da muka ce bamu da ciwo alokacin ne bazamu warke ba. Yakub wani mai kaunar salama ne, wasikar sasanci ga al'umma, wadda ya bayar a lokaci mahimmi cikin tarihi; amma a wannan lokacin basu saurara ba. shin zamu saurara a yau?

A yau, muna da duniya cike da rarrabuwa, ra'ayin sonkai na kasashe da tashin hankali, wanda yake barin mutane da yawa cikin wahala. Sasancin yana da sauki, koda yake yana nufin daukar gicciyen mu da kuma bin Kiristi. Wannan shine ainihin babban labarin da muke rayuwa ciki: "Mutane da yawa suna taimakon wadansu cikin bukatunsu na kullum, komai irin addinisu da kuma irin siyasarsu. Amadadin yin gaddama, mutane suna lura da 'yan'uwansu, kuma suna mantawa da banbancinsu. A maimakon neman matsala da kasar mu da kuma irin abubuwan da suke faruwa, mutane suna godewa Allah domin rayuwarsu da kuma darajarsa. Idan wannan ya cigaba yanayin zai zama da aminci kwarai, yayinda al'ummarmu zata cigaba da inganta."

"Yayinda nake yunwa kuma kun cida ni." Kiristi ya kira duk masu wahalar da masubinsa, makwabtanmu. Masu sa bukatun mutane gaban ra'ayinmu na

rikau da kuma dalilan rarrabuwa a hanyar gaskiya ta ikkilisiya. Muka ce, “Yaya gameda bangaskiyar mu, yaya gameda akidarmu?” wannan itace hanyar da muka kafa bangaskiyar mu, tawurin yin rayuwa da nuna ta.

Shugaban kasar Roma mara addini Emperor Julian (na karni na hudu) yace: “(Bangaskiyar masubi) an karfafa ta sosai tawurin sujadar kauna da ake yiwa baki, da kuma tawurin lura da biznewar wanda ya mutu. Wani abun kunya ne cewa babu wani ba Yahude ko daya mabaraci, da kuma mutanen Galili marasa alloli (wato wadanda yake kira masubi kenan saboda basa yin bautar gumaka ba) suna lura ba da talakawansu kadai ba, amma har da namu, yayinda wadanda suke namu ke neman taimako abanza wanda zamuyi masu.”

Masubi sun kaunaci da kuma lura da Yahudawa da marasa addini, domin su ma mutane ne. Domin yin gasa da masubi Julian ya cigaba da kawo chanji cikin masujadun marasa addini da kuma zaman jin dadin jama’a cikin dukan mulkinsa. Wannan masubi basu tada hankali ba; suka bauta. Lokacin da Romawa suka jefar da ‘ya’yansu jarirai domin su mutu, masubi suka dauke su domin su rike su har suyi girma. Lokacin da mutane ke mutuwa ta annoba, masubi suka yi kasadar rayuwarsu domin su lura da su. Haka da misalin ya cigaba; wannan shine yadda suka chanza duniyar su. Ta wurin yin rayuwar bangaskiyarsu, ba tawurin tashin hankali ba.

Gameda Yesu da kuma Yakub, kamar yadda yake a al’adun Yahudawa, bada gaskiya na nufin aikatawa. “Idan ku ‘ya’yan Ibrahim ne zakuyi aikin ubanku Ibrahim.”Yayinda bishara ke maganar bangaskiya kan Yesu wannan na nufin karbarsa amatsayin Ubangiji, wanda ke nufin zama almajirinsa. Bada gaskiya ba shi da banbanci da yin tuba da kuma sabuwar hanyarsa ta rayuwa. Bangaskiya da aiyyuka su abu daya ne, wanda ruhunsa ke izawa. Ba aiyyukan al’adun addini ba, amma aiyyukan Ubanmu wanda ke cikin sama, bin aiyyukansa kamar yadda muka gani cikin Kiristi.

*2. Menene muke baiwa daraja?*

A kwanaki da lokaci wanda akwai shan wahala da yawa cikin duniya, yayinda al'ummai ke bukatar warkarwa da lura, menene muke baiwa daraja? Menene muke lura da shi sosai? Idan muka cigaba da lura da bukatunmu kadai, banda bukatun wadansu, al'umman mu zasu kara shiga cikin rashin lura, rarrabuwa da kuma tashin hankali.

Bari mu kashe dukiyarmu kadan kan gine-ginen mu da kuma kari kan lura da bukatun gwauraye, marayu da kuma 'yan gudun hijira; iyaye dake su kadai; yara masu bukatu; miskinan tsofaffi. Kada muyi lura kan masubi da ke cikin jama'ar mu kawai, amma harda musulmi da kuma bukatunsu a matsayin mutane. Bari muje wurin dattawan musulmi cikin jama'ar mu(har ma a gabas) kuma mu zauna muyi Magana da su. Mu nemi hanyoyin da zamu yi tafiya da kuma taimakon al'ummar su. Bari mu koma lokacin da musulmi da Kirista suka nuna lura da juna a wuraren da suke zama. Zamu kaunaci sauran mutane koda sun karbi bishara ko a'a. Wannan itace shaida ta ainihi.

Ba wai yin wa'azin bishara ta nuna lurar jiki kawai ba. Wannan baya yin aiki ba. Ana maganar ainihin lura ta kanta. Wato yin rayuwa irin rayuwar masubi. Bishara da ruhaniya ne ke chanza zukata. An kira mu mu nuna wannan chanji a zukatanmu, yayinda muke yada gaskiyarsa cikin kauna.

Lura da sauran mutane ya zama damuwar mu ta farko da kuma yin amfani da lokaci da dukiyar mu. Wannan shine daukar alhaki na iyaye. Mu iyaye da kuma shugabanni ne cikin al'ummar mu. Me yasa muke ba abubuwa daraja fiye da mutane? Domin muna baiwa daukakar kanmu daraja. Yawanci gine-gine da kuma "nasara"cikin idanuwan duniya ke bamu daraja. Mutane zasu tambaya menene muka samu, menene zamu iya nunawa? Yesu zai tambaye mu, menene muka ba daraja, kuma zai baiwa kansa amsa da tabbacin abinda mukayi da rayuwarmu a hakikanin lura da wadansu (Matiyu 25:34-46).

Mutane suna da daraja sosai ga Allah saboda haka kuma dole su zama da daraja garemu. Har sai munkai ga wannan irin rayuwar, al'ummar mu bazasu warke ba. yayinda muka tuba daga wannan yanayi, dukan kome a duniya gameda warkarwa da sasanci zasu iya yiwuwa. "Za'a kira ku masu yin gyaran cin amana."

Domin haka kada mu dauki manyan wuraren zama a wurin taro, amma mu mika kanmu a matsayin bayi masu farinciki, masu kaunar kowanne mutum dake kewaye da su da kuma halin dattijo cikin kauna a matsayin kokarin da muke faman yi. Idan mai keken hawa yazo ikkilisiyar mu, shi ko ita, suna da daraja kamar kowanne mutum kuma ya kamata su ji dadi ajiye kekensu a wurinda ake ajiya mai daraja kamar yadda pasto yake yi. Muna bukatar al'ada inda zamu nuna kauna ga juna da kuma baiwa junanmu daraja, ko mai matsayin mu, ko mai jinsin mu, ko mai girman bangaskiyar mu, ko mai kowanne irin abu. Wannan shine abunda Yakub ya koyar, da kuma wannan ne zai warkar da kasar mu.

Wannan lokacin yin addu'a ne da kuma lokaci na chanji na ainihi daga zuci zuwa waje. Wannan shine Yesu yayi Magana gameda kasar mu, yadda mulkin Allah yazo kuma ya kawo mu cikin kasar sa mai kyau. Almajiranci shine ganewa da kaunar 'yan'uwanmu maza da mata cikin Kiristi, da kuma kauna da lura domin makiyanmu. Wannan shine Yesu ya koyar a lokacin wa'azin kan dutse. Kamar yadda wani aboki yace, "ceto wani aiki ne na sabuntawa, ban a kwashewa ba."

"Ku shiga ta kunkuntar kofa." (Matiyu 7:13) waccece kunkuntar kofa? Aya ta baya tace: "Saboda haka duk abinda kuke so mutane su yi muku, kuma sai kuyi musu. Domin wannan shine Attaura da koyarwar annabawa." Yesu hakika yace zamu yi "aiki da karfin mu sosai" domin yin wannan. Haka kuma cikin Luka, "Ku shiga ta cikin kunkuntar kofa….. domin mutane da yawa zasu ce Ubangiji, Ubangiji amma ba zasu shiga ba." Da kuma cikin Matiyu 25, kunkuntar kofa, "Ubangiji, yau she ne muka ganka kana ji yunwa kuma muka ciyar da kai…..?" Kunkuntar kofa: 'ya'yansa. Bangaskiya bata kawar da

wannan ba, amma bangaskiya ta ainihi tana kawo wannan ‘ya’yan. Shin wannan irin na wannan mulkin: kwayar hatsin tana cikin ‘ya’yan.